سُورَةُ الأَنبِيَاءِ
آيَاتُهَا ١١٢ — تَرْتِيبُهَا ٢١

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

اقْتَرَبَ لِلنَّاسِ حِسَابُهُمْ وَهُمْ فِي غَفْلَةٍ مُّعْرِضُونَ ١ الجزء ١٧ الحزب ٣٣
مَا يَأْتِيهِم مِّن ذِكْرٍ مِّن رَّبِّهِم مُّحْدَثٍ إِلَّا اسْتَمَعُوهُ وَهُمْ
يَلْعَبُونَ ٢ لَاهِيَةً قُلُوبُهُمْ ۗ وَأَسَرُّوا النَّجْوَى الَّذِينَ
ظَلَمُوا هَلْ هَٰذَا إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ ۖ أَفَتَأْتُونَ السِّحْرَ وَأَنتُمْ
تُبْصِرُونَ ٣ قَالَ رَبِّي يَعْلَمُ الْقَوْلَ فِي السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ ۖ
وَهُوَ السَّمِيعُ الْعَلِيمُ ٤ بَلْ قَالُوا أَضْغَاثُ أَحْلَامٍ بَلِ
افْتَرَاهُ بَلْ هُوَ شَاعِرٌ فَلْيَأْتِنَا بِآيَةٍ كَمَا أُرْسِلَ الْأَوَّلُونَ
٥ مَا آمَنَتْ قَبْلَهُم مِّن قَرْيَةٍ أَهْلَكْنَاهَا ۖ أَفَهُمْ يُؤْمِنُونَ
٦ وَمَا أَرْسَلْنَا قَبْلَكَ إِلَّا رِجَالًا نُّوحِي إِلَيْهِمْ ۖ فَاسْأَلُوا أَهْلَ
الذِّكْرِ إِن كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ٧ وَمَا جَعَلْنَاهُمْ جَسَدًا
لَّا يَأْكُلُونَ الطَّعَامَ وَمَا كَانُوا خَالِدِينَ ٨ ثُمَّ صَدَقْنَاهُمُ
الْوَعْدَ فَأَنجَيْنَاهُمْ وَمَن نَّشَاءُ وَأَهْلَكْنَا الْمُسْرِفِينَ ٩
لَقَدْ أَنزَلْنَا إِلَيْكُمْ كِتَابًا فِيهِ ذِكْرُكُمْ ۖ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ١٠



# Suratul Anbiya'i

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Bayanin dukkan saqonnin Annabawa iri xaya ne, ta hanyar tunatar wa akan halin da Annabawan suka samu kansu a ciki da saqon da suka zo da shi, wanda iri xaya ne, shi ne bautawa Allah shi kaxai.**

**Tafsir:**

**(1) lokacin yin hisabi ga mutane dangane da ayyukansa a ranar alqiyama ya kusa, alhali kuwa su, su suna cikin rafkannuwa, kuma sun juya baya ga lahira, saboda saboda shagalarsu da duniya da barin su ga lahira. (2) Babu wani abin karantawa da zai zo musu daga Ubangijinsu, wanda yake sabon saukowa, face sai sun saurare shi, saurare bana amfani ba, kurum sauraren wasa da rashin damuwa da shi. (3) Suna sauraransa ne alhali zukatansu suna rafkanannu dangane da shi, kuma waxanda suka zalunci kawunansu da kafirci suna ganawa a sirrance a tsakaninsu da faxin cewa: “Wannan mai iqrarin cewa shi Manzo ne, shin wani abu ne shi ban da kasancewarsa mutum irinku, ba shi da wani fifiko a kanku?! Kuma ai tsafi ya zo da shi! Yanzu zaku yi masa biyayya alhali kuna sane da cewa shi mutum ne irinku, kuma tsafi ne abin da ya zo da shi?!”. (4) Manzon Allah (S.A.W) ya ce: “Ubangijina ya san abin da kuke voyewa a tsakaninku na zance, domin ya san duk zancen da wani zi yi a sammai da qassai, kuma Shi mai jin zancen bayinsa ne, mai cikakken sanin ayyukansu ne, kuma da sannu zai yi musu sakayya a kansu”. (5) Bari dai, sun yi kai-kawo akan abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi: “Wani lokacin su ce yaye-yayen mafarki ne, wanda ba shi da fassara”. Wani lokacin su ce: “Shi ya qirqire shi, ba shi da wani asali” Wani lokacin su ce: “Shi mawaqi ne, kuma in har shi mai gaskiya ne, to ya kawo mana wata mu'u’jiza irin yadda Manzanni na farko suka yi, saboda lallai su sun kawo mu'u’jizozi, irin su sandar Annabi Musa da taguwar Annabi Salihu”. (6) Babu wata alqarya gabaninsu wadda ta tava neman a kawo mata mu'u’jiza, kuma ta yi imani bayan an saukar da mu'’ujizar yadda ta nema. Duk sun qaryata su ne, don haka sai muka halaka su. Shin waxannan za su yi imani ne?!.**

**(7) Kuma bamu tava turo wani manzo ba gabaninka – Ya kai wannan Manzo - face mazaje ne su kuma daga cikin mutane, waxanda muke musu wahayi, ba mu tava tayar da su a matsayin Mala'iku ba. Ku tambayi masana ma'abota littafi magabatanku, in ku baku san haka ba.**

**(8) Ba mu saka manzannin da muke aiko su ba, wasu gangar jiki ne marasa cin abinci ba, A'a, suna cin abinci kamar yadda wasunsu suke ci, kuma ba su kasance masu wanzuwa a duniya ba, su zama ba sa mutuwa ba.**

**(9) Sannan mun tabbatar wa Manzanninmu abin da muka yi musu alqawarinsa, muka tserar da su da wanxanda muka ga dama cikin Muminai daga halaka, muka halakar da masu qetare iyaka da kafirce wa Allah da zaqewa a cikin savonsa. (10) Lallai mun saukar muku da Alqur'ani wanda akwai xaukaka da abin alfaharinku a cikinsa, in kun bayar da gaskiya da shi, kuka yi aiki da abin da ke cikinsa, shin baza ku hankalci hakan ba, ku yi gaggawa zuwa imani da shi da yin aiki da abin da ya qunsa ba?!.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kusantowar tashin alqiyama, abin da ya ke wajabta yi mata shiri. 2 - Shagaltuwar zukata da wargi, yana kawar da su daga tafarkin gaskiya 3 - Kewayewar ilimin Allah da duk abin da yake fitowa daga bayinsa na zance ko aiki. 4 - Savanin Mushirikai akan matsayin Annabi (S.A.W) yana nuna fagamniyarsu da ruxunsu. 5 - Allah yana tare da Manzanninsa da Muminai wajen qarfafa musu gwiwa da ba su taimako a kan maqiya. 6 - Alqur'ani xaukaka ne da izza ga duk wanda ya yi imani da shi, kuma ya yi aiki da shi.**

وَكَمۡ قَصَمۡنَا مِن قَرۡيَةٖ كَانَتۡ ظَالِمَةٗ وَأَنشَأۡنَا بَعۡدَهَا قَوۡمًا
ءَاخَرِينَ ١١ فَلَمَّآ أَحَسُّواْ بَأۡسَنَآ إِذَا هُم مِّنۡهَا يَرۡكُضُونَ ١٢
لَا تَرۡكُضُواْ وَٱرۡجِعُوٓاْ إِلَىٰ مَآ أُتۡرِفۡتُمۡ فِيهِ وَمَسَٰكِنِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ
تُسۡـَٔلُونَ ١٣ قَالُواْ يَٰوَيۡلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ١٤ فَمَا زَالَت تِّلۡكَ
دَعۡوَىٰهُمۡ حَتَّىٰ جَعَلۡنَٰهُمۡ حَصِيدًا خَٰمِدِينَ ١٥ وَمَا خَلَقۡنَا
ٱلسَّمَآءَ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا لَٰعِبِينَ ١٦ لَوۡ أَرَدۡنَآ أَن نَّتَّخِذَ
لَهۡوٗا لَّٱتَّخَذۡنَٰهُ مِن لَّدُنَّآ إِن كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٧ بَلۡ نَقۡذِفُ بِٱلۡحَقِّ
عَلَى ٱلۡبَٰطِلِ فَيَدۡمَغُهُۥ فَإِذَا هُوَ زَاهِقٞۚ وَلَكُمُ ٱلۡوَيۡلُ مِمَّا تَصِفُونَ
١٨ وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَنۡ عِندَهُۥ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ
عَنۡ عِبَادَتِهِۦ وَلَا يَسۡتَحۡسِرُونَ ١٩ يُسَبِّحُونَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ
لَا يَفۡتُرُونَ ٢٠ أَمِ ٱتَّخَذُوٓاْ ءَالِهَةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ هُمۡ يُنشِرُونَ ٢١
لَوۡ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَاۚ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلۡعَرۡشِ
عَمَّا يَصِفُونَ ٢٢ لَا يُسۡـَٔلُ عَمَّا يَفۡعَلُ وَهُمۡ يُسۡـَٔلُونَ ٢٣ أَمِ ٱتَّخَذُواْ
مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةٗۖ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡۖ هَٰذَا ذِكۡرُ مَن مَّعِيَ وَذِكۡرُ
مَن قَبۡلِيۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٱلۡحَقَّۖ فَهُم مُّعۡرِضُونَ ٢٤



**(11) Alqrayu guda nawa ne muka halaka su, saboda zaluntar kawunansu da kafirci, muka halicci wasu mutanen daban a bayansu!.**
**(12) Lokacin da halakakkun suka yi ido huxu da azabarmu ta qare dangi, sai kawai suka fara sauri suna qoqarin guduwa daga halaka.**
**(13) Sai a kira su da izgili a ce musu: "Kar ku gudu, ku dawo zuwa abin da kuka kasance a cikin na bushasha da abubuwan jin xaxinku da gidajenku, ko a tambayeku wani abu na duniyarku.**
**(14) Sai Waxannan azzalumai suka ce, suna masu iqrari da zunubansu: "Kaiconmu da hasararmu, lallai mun kasance azzalumai saboda kafircewar mu ga Allah.**
**(15) Ba za su gushe ba suna tabbatar da zunubansu, suna wa kawunansu addu'ar halaka, suna ta maimaita ta, har sai mun mayar da su kamar shukar da aka girbe, matattu ba sa motsi.**
**(16) Ba mu halicci sammai da qassai da abin da ke tsakaninsu don wasa ba!. Mun halicce su ne saboda su yi nuni zuwa ga ikonmu.**
**(17) Da mun ga damar xaukan wani a matsayin xa ko abokiyar zama, da zamu xauka ne cikin abubuwan da suke wurinmu. Amma ba zamu yi hakan ba, domin mun tsarkaka daga yin hakan.**
**(18) Bari dai, muna jefa gaskiyar da muke yin wahayinta zuwa ga Manzanmu ne a kan qaryar ma'abota kafirci, sai ta yi daga-daga da ita, sai kawai ya zama ta gushe, babu ita. Kuma tabbas – Ya ku masu cewa Allah ya xauki wani a matsayin xa, ko abokiyar zama- kuna da wata azaba ta halaka a sakamakon yadda kuke siffanta Allah da abin da bai dace da shi ba.**
**Yayin da xaukar abokiyar zama da xa yana nuna buqata ce, sai Allah ya bayyana cewa shi ne mamallakin wannan halitta gaba xaya, ya ce:**
**(19) Allah mai tsarki shi kaxai ne yake mallakar sammai da qassai, kuma waxanda suke a wurinsa na Mala'iku ba sa girman kai cikin bautarsa, kuma ba sa qosawa ko gajiya da bautarsa.**
**(20) Suna dauwama akan tsabihi ga Allah, ba sa qosawa.**
**(21) Amma Mushirikai sun xauki wasu ababen bauta koma bayan Allah, waxanda ba sa iya raya mamata. To ta yaya za a bauta wa wanda ba zai iya wannan ba?!.**
**(22) Da a ce akwai abubuwan bauta masu yawa cikin sammai da qassai, da sun lalace saboda jayayya a kan mulki tsakanin abubuwan bautar. Amma dai lamarin ba haka yake ba. Tsarki ya tabbata ga Allah mai Al'arshi daga barin abin da mushirikai suke siffata shi da shi, na qarya, cewa: yana da abokan tarayya.**
**(23) Allah shi ne makaxaici cikin mulkinsa da zartarwarsa, babu wanda ya isa ya tambaye shi dangane da mulkinsa da abin da ya zartar. Shi ne zai tambayi bayinsa dangane da ayyukansu, kuma ya saka musu a kansu.**
**(24) Bari sai, sun xauki wasu abubuwan bauta koma bayan Allah, to ka ce da waxannan mushirikan, - Ya kai wannan Manzo-: "Ku kawo hujjarku akan cancantar waxannan da bauta. Ni ga littafin da aka saukar mini, ga littattafan da aka saukar wa Manzanni gabani na, dukkaninsu ba ku da hujja a cikinsu. Bari dai, kawai mafi yawan mushirikai ba su dogara da komai ba sai jahilci da makauniyar biyayya, don haka suka kasance masu juya baya ga karvar gaskiya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Zalunci sababin halaka ne a mataki na xaixaiku da na jama'u.**
**2 - Allah bai halicci wani abu kara zube ba, domin shi Allah Mai tsarki ya tsarkaka daga wargi.**
**3 - Bayar da nasara ga gaskiya da daqile qarya sunna ce ta Ubangiji.**
**4 - Vacin aqidar shirka ta dalilin rashin yiwuwar samuwar abin guda biyu (Wato dalilin tamaanu'u).**

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ
إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥ وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَلَدٗاۗ سُبۡحَٰنَهُۥۚ
بَلۡ عِبَادٞ مُّكۡرَمُونَ ٢٦ لَا يَسۡبِقُونَهُۥ بِٱلۡقَوۡلِ وَهُم
بِأَمۡرِهِۦ يَعۡمَلُونَ ٢٧ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡ
وَلَا يَشۡفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ٱرۡتَضَىٰ وَهُم مِّنۡ خَشۡيَتِهِۦ مُشۡفِقُونَ
الحزب ٣٣ ٢٨ ۞ وَمَن يَقُلۡ مِنۡهُمۡ إِنِّيٓ إِلَٰهٞ مِّن دُونِهِۦ فَذَٰلِكَ نَجۡزِيهِ
جَهَنَّمَۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٩ أَوَلَمۡ يَرَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ
أَنَّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ كَانَتَا رَتۡقٗا فَفَتَقۡنَٰهُمَاۖ وَجَعَلۡنَا
مِنَ ٱلۡمَآءِ كُلَّ شَيۡءٍ حَيٍّۚ أَفَلَا يُؤۡمِنُونَ ٣٠ وَجَعَلۡنَا فِي ٱلۡأَرۡضِ
رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِهِمۡ وَجَعَلۡنَا فِيهَا فِجَاجٗا سُبُلٗا لَّعَلَّهُمۡ
يَهۡتَدُونَ ٣١ وَجَعَلۡنَا ٱلسَّمَآءَ سَقۡفٗا مَّحۡفُوظٗاۖ وَهُمۡ عَنۡ
ءَايَٰتِهَا مُعۡرِضُونَ ٣٢ وَهُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمۡسَ
وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ فِي فَلَكٖ يَسۡبَحُونَ ٣٣ وَمَا جَعَلۡنَا لِبَشَرٖ مِّن قَبۡلِكَ
ٱلۡخُلۡدَۖ أَفَإِيْن مِّتَّ فَهُمُ ٱلۡخَٰلِدُونَ ٣٤ كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ
ٱلۡمَوۡتِۗ وَنَبۡلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلۡخَيۡرِ فِتۡنَةٗۖ وَإِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ٣٥



**(25) Ba mu aiko da wani Manzo gabaninka ba – Ya kai wannan Manzo - face sai mun yi masa wahayi cewa babu abin bautawa da gaskiya sai ni, (Allah) ni kaxai, don haka ku bauta mini ni kaxai, kar ku yi min tarayya da wani.**

**(26) Kuma Mushirikai sun ce: “Allah ya xauki Mala'iku a matsayin ‘ya'yansa mata!. Allah ya tsarkaka daga wannan abin da suke faxa na qarya. Mala'iku bayin Allah ne, masu girma a wurin Allah, masu kusanci gare shi.**

**(27) Ba sa wuce gaban Ubangijinsu da wata magana, don ba sa faxar wani zance sai ya umarce su, kuma da umarninsa suke aiki, ba sa sava masa umarni.**

**(28) Yana sane da ayyukansu da suka gabata, da waxanda za su yi nan gaba, kuma ba sa roqon ceto sai da izininsa ga wanda ya yarda a nema masa ceton. Kuma su, saboda tsoron Allah, masu kiyayewa ne, ba sa sava masa umarni ko hani.**

**(29) Da wani cikin Mala'iku zai faxa misali ya ce: “Ni abin bauta ne koma bayan Allah”, to lallai da mun saka masa akan wannan zancen da azabar wutar Jahannama a ranar alqiyama, kuma ya daxe a cikinta. Kuma irin wannan sakamakon muke yi ga azzalumai masu zaluntar kawunansu da kafirci da shirka ga Allah.**

**(30) Shin kafirai ba su san cewa sammai da qassai da, sun kasance a haxe ba ne, babu sarari a tsakaninsu ballantana ruwan sama ya sauka, sai muka raba su, sannan muka sanya ruwan saman da ke saukowa zuwa qasa sanadin rayuwar duk wata dabba da tsiro ba. Shin ba za su yi la'aari da wannan ba, su yi imani da Allah shi kaxai?!.**

**(31) Muka halicci duwatsu tabbatattu a qasa, saboda kar ta motsa, ta girgiza da waxanda suke a kanta, kuma muka sanya hanyoyi masu faxi cikinta, domin su gane hanya cikin tafiye -tafiyensu zuwa biyan buqatunsu.**

**(32) Muka sanya sama ta zama rufi wanda aka kare daga faxuwa, kuma ba tare da ginshiqai ba, kuma muka kare ta daga satar ji na shaixanu, amma mushirikai masu kawar da kai ne ga abubuwan da ke sama na ayoyi –irin su rana da wata- ba sa izina da su.**

**(33) Allah shi ne shi kaxai wanda ya halicci dare don hutu, ya halicci yini don neman abin da zai tsayar da rayuwa, kuma ya halicci rana alamar yini, da wata alamar dare. Kowanne cikin ranar da wata yana gudana a magudanarsa wadda aka keve masa, ba ya goce daga gare shi ko ya kauce.**

**(34) Ba mu sanya wa wani mutum a gabaninka ba – Ya kai wannan Manzo- cewa zai wanzu a gidan duniya! Shin idan ajalinka ya qare a wannan rayuwa ta duniya sai ka mutu, shin waxannan zasu wanzu ne bayanka?! Faufau!.**

**(35) Kowace rai, mumina ko kafira za ta xanxani mutuwa a duniya, kuma Muna jarrabaku ne – Ya ku mutane- a cikin rayuwar duniya da hukunce-hukuncen Shari'ah da ni'imomi da uqubobi, sannan bayan mutuwarku, zuwa gare mu ne kaxai, ba zuwa ga wani ba, za a mayar da ku, sai mu saka muku akan ayyukanku.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsarkake Allah daga xaukan wani a matsayin yaro.**

**2 - Matsayin Mala'iku a wurin Allah shi ne su bayi ne, Allah ya halicce su ne saboda biyayya a gare shi, ba a siffantasu da mazantaka ko matantaka, a'a, bayi ne masu girma.**

**3 - An halicci Sammai da Qasa ne bisa tsarin sannu-sannu: an fara haliccesu a haxe ne sannan aka raba su daga baya.**

**4 - Jarabawa kamar yadda take kasancewa da sharri haka ma tana kasancewa da alheri.**

وَإِذَا رَءَاكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِن يَتَّخِذُونَكَ إِلَّا هُزُوًا أَهَٰذَا
ٱلَّذِي يَذۡكُرُ ءَالِهَتَكُمۡ وَهُم بِذِكۡرِ ٱلرَّحۡمَٰنِ هُمۡ
كَٰفِرُونَ ٣٦ خُلِقَ ٱلۡإِنسَٰنُ مِنۡ عَجَلٖۚ سَأُوْرِيكُمۡ
ءَايَٰتِي فَلَا تَسۡتَعۡجِلُونِ ٣٧ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ
إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٣٨ لَوۡ يَعۡلَمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ حِينَ
لَا يَكُفُّونَ عَن وُجُوهِهِمُ ٱلنَّارَ وَلَا عَن ظُهُورِهِمۡ وَلَا
هُمۡ يُنصَرُونَ ٣٩ بَلۡ تَأۡتِيهِم بَغۡتَةٗ فَتَبۡهَتُهُمۡ فَلَا
يَسۡتَطِيعُونَ رَدَّهَا وَلَا هُمۡ يُنظَرُونَ ٤٠ وَلَقَدِ ٱسۡتُهۡزِئَ
بِرُسُلٖ مِّن قَبۡلِكَ فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ سَخِرُواْ مِنۡهُم مَّا كَانُواْ
بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٤١ قُلۡ مَن يَكۡلَؤُكُم بِٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ
مِنَ ٱلرَّحۡمَٰنِۚ بَلۡ هُمۡ عَن ذِكۡرِ رَبِّهِم مُّعۡرِضُونَ ٤٢
أَمۡ لَهُمۡ ءَالِهَةٞ تَمۡنَعُهُم مِّن دُونِنَاۚ لَا يَسۡتَطِيعُونَ نَصۡرَ
أَنفُسِهِمۡ وَلَا هُم مِّنَّا يُصۡحَبُونَ ٤٣ بَلۡ مَتَّعۡنَا هَٰٓؤُلَآءِ
وَءَابَآءَهُمۡ حَتَّىٰ طَالَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡعُمُرُۗ أَفَلَا يَرَوۡنَ أَنَّا نَأۡتِي
ٱلۡأَرۡضَ نَنقُصُهَا مِنۡ أَطۡرَافِهَآۚ أَفَهُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ٤٤



**(36) Idan waxannan Mushirikai sun gan ka –Ya kai wannan Manzo- basa xaukar ka a bakin komai sai dai abin yi wa izgili, suna saka kyamarka ga mabiyansu suna cewa: "Shin wannan shi ne wanda yake zagin abubuwan bautarku da kuke musu bauta?!" Kuma qari akan izgilin da suke maka, suna jayayya da abin da Allah ya saukar musu na Alqur'ani, kuma suna yin butulci game da abin da ya ba su na ni'imomi, don haka su suka fi cancanta da aibata wa saboda sun haxa kowane irin abu mummuna.**

**(37) An halicci mutum akan gaggawa, don haka yake gaggauto da abubawa kafin lokacin afkuwarsu. Yana da cikin hakan, yadda mushirikai suke gaggawar a yi musu azaba. Da sannu zan gana muku –ya ku masu neman azabata da gaggawa- abin da suke nema na azabar, don haka ba sai kun neme shi da gaggawa ba.**

**(38) Kafiran da suke inkarin tashi bayan mutuwa suna cewa, saboda gaggawa: "Yaushe ne abin da kuke mana alqawainsa – Ya ku Musulmaina tashi bayan mutuwa zai afku ne, in har kun kasance masu gaskiya ne cikin abin da kuke iqrarinsa na faruwarsa?!".**

**(39) Da waxannan kafiran masu inkarin tashi bayan mutuwa zasu san lokacin da ba zasu iya kawar da wuta daga fuskokinsu da bayansu, kuma basu da wani mataimaki da zai taimake su ta hanyar tunkuxe musu wannan azabar, da sun sakankace da haka da ba su nemi a gaggauta musu azaba ba.**

**(40) Wannan wutar da za ayi musu azaba da ita, ba zata zo musu, a lokacin da suna sane da ita ba, zata zo musu ne kwatsam, baza su iya tunkuxe ta ga kawunansu ba, kuma ba za a jinkirta musu ba, ballantana su tuba, har rahama ta same su.**

**Kasancewar Manzon Allah (S.A.W) ya fuskanci izgili da qaryatawar mutanensa, sai Allah ya lallashe shi da faxinsa ce wa: (41) Idan mutanenka sun yi maka izgili to ba kai ne farau a cikin wannan ba. Lallai an yi wa Manzanni gabanin ka – Ya kai wannan Manzo- sai azabar da masu izgilin suke yin izgili a kanta, a duk lokacin da Manzannin suka yi musu alqawarin zuwan ta, ta mamaye su.**

**(42) Ka faxa wa waxannan masu gaggawar a kawo musu azabar - Ya kai wannan Manzo- cewa: "Waye wanda zai kare ku da daddare ko da rana daga abin da Allah mai rahama ya yi nufin ya sauka a kanku na azaba da halaka?!". Bari dai, sun kasance masu kawar da kai ne dangane da wa'azin Ubangijinsu da hujjojinsa, basa yin wani tunani a ciki saboda jahilci da wauta.**

**(43) Ko dai, shin suna da wasu abubuwan bauta ne waxanda zasu kare su daga azabarmu?! Ba zasu iya taimakon kansu da tunkuxe wata cuta ko jawo wani amfani ba. Wanda ba zai iya agaza wa kansa ba, to ta yaya zai agaza wa wani?! Kuma ba za a basu mafaka daga azabarmu ba.**

**(44) Mun ba waxannan kafirai jin daxi, su da iyayensu, da abin da muka shimfixa musu na ni'imominmu, domin mu yi musu talala, har sai da suka kwashe tsawon lokaci a kan hakan, sai suka yaudaru da wannan, suka doge bisa kafircin su. Shin waxannan ruxaxxun, masu gaggauto da azaba a kansu basu san cewa mu muna zakke wa qasa ta bangarorinta daban daban, ta hanyar rinjayar mutanenta, da cin galaba a kansu ba ne, sai su yi la'akari da haka, don kar abin da ya auka a kan wasunsu ya faxa musu?! Waxannan ba masu cin galaba ba ne, su ne ma ake cin galaba a kansu.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Bayanin kafircin wanda yake yin izgili ga Manzan Allah, sawa'un da zance ko aiki ko nuni. 2 - Gaggawa tana daga cikin xabi'un mutum, kuma bi sannu-sannu xabi'a ce mai kyau. 3 - Babu wanda zai kare azabar Allah sai Allah. 4 - Karshen qarya shi ne gushewa, qarshen gaskiya kuma shi ne wanzuwa.**

قُلْ إِنَّمَآ أُنذِرُكُم بِٱلْوَحْيِ ۚ وَلَا يَسْمَعُ ٱلصُّمُّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا
مَا يُنذَرُونَ ٤٥ وَلَئِن مَّسَّتْهُمْ نَفْحَةٌ مِّنْ عَذَابِ رَبِّكَ
لَيَقُولُنَّ يَٰوَيْلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ٤٦ وَنَضَعُ ٱلْمَوَٰزِينَ
ٱلْقِسْطَ لِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ فَلَا تُظْلَمُ نَفْسٌ شَيْـًٔا ۖ وَإِن كَانَ
مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ أَتَيْنَا بِهَا ۗ وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ٤٧
وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ٱلْفُرْقَانَ وَضِيَآءً وَذِكْرًا
لِّلْمُتَّقِينَ ٤٨ ٱلَّذِينَ يَخْشَوْنَ رَبَّهُم بِٱلْغَيْبِ وَهُم مِّنَ ٱلسَّاعَةِ
مُشْفِقُونَ ٤٩ وَهَٰذَا ذِكْرٌ مُّبَارَكٌ أَنزَلْنَٰهُ ۚ أَفَأَنتُمْ لَهُۥ
مُنكِرُونَ ٥٠ ۞ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَآ إِبْرَٰهِيمَ رُشْدَهُۥ مِن قَبْلُ وَكُنَّا نصف الحزب ٣٣
بِهِۦ عَٰلِمِينَ ٥١ إِذْ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَا هَٰذِهِ ٱلتَّمَاثِيلُ ٱلَّتِىٓ
أَنتُمْ لَهَا عَٰكِفُونَ ٥٢ قَالُوا۟ وَجَدْنَآ ءَابَآءَنَا لَهَا عَٰبِدِينَ ٥٣ قَالَ
لَقَدْ كُنتُمْ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُمْ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ٥٤ قَالُوٓا۟ أَجِئْتَنَا
بِٱلْحَقِّ أَمْ أَنتَ مِنَ ٱللَّٰعِبِينَ ٥٥ قَالَ بَل رَّبُّكُمْ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ٱلَّذِى فَطَرَهُنَّ وَأَنَا۠ عَلَىٰ ذَٰلِكُم مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٥٦
وَتَٱللَّهِ لَأَكِيدَنَّ أَصْنَٰمَكُم بَعْدَ أَن تُوَلُّوا۟ مُدْبِرِينَ ٥٧



**(45) Ka ce musu – Ya kai wannan Manzo- Ni fa ina tsoratar da ku azabar Allah ne fa kawai -Ya ku mutane- da abin da Ubangijina yake mini wahayinsa, amma kurame ba za su ji abin da ake kiransu zuwa gare shi, ji na karva ba, idan aka tsoratar da su daga azabar Allah.**

**(46) Kuma Wallahi idan wani kaso na azabar Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- ta shafi waxannan masu gaggauto azabar, to lallai zaka ji suna cewa a lokacin: " Kaiconmu, wayyo mun yi hasara mun halaka, lallai mun kasance azzalumai, saboda shirka da Allah, da qaryata abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi".**

**(47) Zamu kafa ma'aunai na gaskiya ga mutane a alqiyama, domin a auna ayyukansu da shi, ba za a zalunci wata rai ba a ranar, ta hanyar tauye mata ladanta, ko qara mata laifukanta. Koda kuwa abin da za a auna xan kaxan ne, irin wanda nauyinsa gwargwadon nauyin qwayar komayya ne, to sai mun zo da shi. Kuma mun isa cikakkun masu qididdiga da zamu gididdige ayyukan bayinmu.**

**(48) Mun ba wa Annabi Musa da Haruna (A.S) Attaura, tana mai rarrabe tsakanin gaskiya da qarya, tsakanin halal da haram, kuma shiriya ga masu imani, kuma tunatarwa ga masu tsoron Ubangijinsu.**

**(49) Waxanda suke jin tsoron uqubar Ubangijinsu wanda suka yi imani da shi, duk da cewa ba su gan shi ba. Kuma dangane da tashin alqiyama su masu jin tsoro ne.**

**(50) Wannan Alqur'anin da aka saukar wa Annabi Muhammad (S.A.W) wa'azi ne ga duk wanda ya so ya wa'azantu da shi, mai albarka, mai yawan amfani da alheri, Shin duk da hakan kuna inkarinsa, ba zaku yarda da abin da yake cikinsa ba, ku yi aiki da shi ba?!**

**(51) Haqiqa mun ba wa Annabi Ibrahim (A.S) hujja akan mutanensa tun a yarintar sa, kuma mun san shi, don haka sai muka ba shi abin da ya cancance shi cikin iliminmu, na hujja a kan mutanensa.**

**(52) yayin da ya cewa babansa Azara da mutanensa: "Waxanna gumaka ne waxannan kuka sassaka da hannuwanku, kuma kuke dogewa akan bauta musu?".**

**(53) Sai mutanensa suka ce: "Mun samu iyayenmu suna bauta musu ne, don haka sai muke bauta musu don koyi da su".**

**(54) Annabi Ibrahim (A.S) ya ce musu: "Haqiqa kun kasance – Ya ku Mabiya - da ku da iyayenku waxanda kuka yi musu biyayya a cikin vata mabayyani daga tafarkin gaskiya".**

**(55) Sai mutanensa suka ce masa: "Shin ka zo mana da maganar gaskiya ne, yayin da ka faxi wannan, ko dai ka kasance cikin masu wasa ne?".**

**(56) Sai Annabi Ibrahim (A.S) ya ce: "A'a, na zo muku da gaskiya ne ba wasa ba. Ubangijinku shi ne Ubangijin sammai da qassai wanda ya halicce su, ba tare da wani samfuri da ya gabata ba. Kuma ni xaya ne cikin masu bayar da shaida cewa shi ne Ubangijinku da sammai da qassai. Gumakanku kuwa ba su da wani rabo cikin wannan".**

**(57) Annabi Ibrahim (A.S) ya faxa ta yadda mutanensa za su ji shi, ya ce: "Na rantse da Allah sai na shirya wa gumakanku abin da ba zaku ji daxinsa ba, bayan kun tafi wurin bikin ku, kun bar su".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Amfanin yin iqrari da zunubi yana rataye ne da lazimtar tuba gabanin lokacinta ya qure.**

**2 - Tabbatar da adalci ga Allah, da kore zalunci daga gare shi. 3 - Mahimmancin qarfin hujja cikin da'awah zuwa ga Allah. 4 - Cutar makauniyar biyayya. 5 - Bi a sannu-sannu wajen gyara varna, da farawa da mafi sauki, sannan wanda yake biye masa. Annabi Ibrahim (A.S) ya fara gyara varnar mutanensa ne da baki, da bayyana hujja, sannan ya je zuwa ga gyara da hannu.**

فَجَعَلَهُمْ جُذَاذًا إِلَّا كَبِيرًا لَّهُمْ لَعَلَّهُمْ إِلَيْهِ يَرْجِعُونَ
٥٨ قَالُوا مَن فَعَلَ هَٰذَا بِآلِهَتِنَا إِنَّهُ لَمِنَ الظَّالِمِينَ ٥٩
قَالُوا سَمِعْنَا فَتًى يَذْكُرُهُمْ يُقَالُ لَهُ إِبْرَاهِيمُ ٦٠ قَالُوا فَأْتُوا
بِهِ عَلَىٰ أَعْيُنِ النَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَشْهَدُونَ ٦١ قَالُوا أَأَنتَ
فَعَلْتَ هَٰذَا بِآلِهَتِنَا يَا إِبْرَاهِيمُ ٦٢ قَالَ بَلْ فَعَلَهُ كَبِيرُهُمْ
هَٰذَا فَاسْأَلُوهُمْ إِن كَانُوا يَنطِقُونَ ٦٣ فَرَجَعُوا إِلَىٰ
أَنفُسِهِمْ فَقَالُوا إِنَّكُمْ أَنتُمُ الظَّالِمُونَ ٦٤ ثُمَّ نُكِسُوا
عَلَىٰ رُءُوسِهِمْ لَقَدْ عَلِمْتَ مَا هَٰؤُلَاءِ يَنطِقُونَ ٦٥ قَالَ
أَفَتَعْبُدُونَ مِن دُونِ اللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكُمْ شَيْئًا وَلَا
يَضُرُّكُمْ ٦٦ أُفٍّ لَّكُمْ وَلِمَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ اللَّهِ
أَفَلَا تَعْقِلُونَ ٦٧ قَالُوا حَرِّقُوهُ وَانصُرُوا آلِهَتَكُمْ إِن كُنتُمْ
فَاعِلِينَ ٦٨ قُلْنَا يَا نَارُ كُونِي بَرْدًا وَسَلَامًا عَلَىٰ إِبْرَاهِيمَ
٦٩ وَأَرَادُوا بِهِ كَيْدًا فَجَعَلْنَاهُمُ الْأَخْسَرِينَ ٧٠ وَنَجَّيْنَاهُ
وَلُوطًا إِلَى الْأَرْضِ الَّتِي بَارَكْنَا فِيهَا لِلْعَالَمِينَ ٧١ وَوَهَبْنَا
لَهُ إِسْحَاقَ وَيَعْقُوبَ نَافِلَةً وَكُلًّا جَعَلْنَا صَالِحِينَ ٧٢



**58 Sai Annabi Ibrahim (A.S) ya kakkarya gumakansu har suka zama gunduwa gunduwa, qanana, ya bar babbansu domin in sun dawo su tambaye shi, wa ya kakkarya su.**

**59 Yayin da suka dawo, suka samu gumakansu an rushe su, sai suka tambayi junansu: "Wa ya kakkarya mana abubuwan bautarmu?, Lallai wanda ya kakkarya su, yana cikin azzalumai, saboda ya wulaqanta abin da ya cancanci girmamawa da tsarkakewa".**

**60 Sai Wasu daga cikinsu suka ce: "Mun ji wani saurayi yana ambatansu da muni, yana aibata su, ana kiransa Ibrahim, tana iya yiwu wa shi ne ya kakkarya su".**

**61 Sai manyansu suka ce: "Ku kawo Ibarahim a idon mutane a wajen taro, domin su bayar da shaida akan iqrarinsa da abin da ya aikata, saboda iqrarinsa xin ya zama hujjarku a kansa".**

**62 Sai suka kawo Annabi Ibrahim (A.S) suka tambaye shi: "Shin kai ne ka aikata wannan aika-aika da gumakan mu, ya kai Ibrahim?!".**

**63 Sai Annabi Ibrahim ya ce, - Yana mai musu izgili, yana nuna musa gajiyawar gumakansu a gaban mutane -: "Ban aikata haka ba, babbansu ne ne ya yi aikata, ku tambaye gumakanku in sun kasance suna magana".**

**64 Sai suka dawo cikin hayyacinsu da tunani da la'akari, sai ya bayyana gare su cewa, ai gumakan su basa amfani, basa cutarwa, don haka su ne azzalumai da suka bauta musu koma bayan Allah.**

**65 Sannan suka sake komawa zuwa ga taurin kai da qin gaskiya, suka ce: "Haqiqa ai kana da tabbas – Ya kai Ibrahim - cewa waxannan gumakan ba sa magana, don me zaka ce mana mu tambaye su?" Suna nufin hakan hujja ce a gare su, sai ya zama hujja a kansu.**

**66 Annabi Ibrahim (A.S) ya ce - Yana mai musu inkari-: "Ashe za ku bauta wa wasu gumaka koma bayan Allah, waxanda ba sa tsinana muku amfanin komai, ko su cutar da ku, ba ma za su iya tunkuxe wa kawunansu cutarwa ba, ko su jawo musu amfani?!".**

**67 Tir da ku, tir da abin da kuke bautawa koma bayan Allah, na waxannan gumakan da ba sa amfani ko su cutar, shin ba zaku yi hankali ba, ku daina bauta musu?".**

**68 Yayin da suka gaza fuskantar sa da hujja, sai suka koma zuwa ga qarfi. Suka ce: "Ku qone shi da wuta, don taimakon gumakan ku da ya rushe su, ya kakkarya su, in har za ku yi masa uquba mai tsanani".**

**69 Sai suka kunna wuta, suka jefa shi a cikinta. Sai muka ce: "Ya ke wuta. ki kasance sanyi da aminci ga Ibrahim", sai ta kasance hakan, bai cutu ba.**

**70 Mutanen Annabi Ibrahim (A.S) sun yi nufin makirci gare shi, na su qone shi, sai muka vata makircinsu, muka sanya su suka zama halakakku, Waxanda aka rinjaya.**

**71 Muka quvutar da shi tare da Annabi Lux (A.S), Muka fitar da su zuwa garin Sham, garin muka yi masa albarka, da irin Annabawan da muka tura su cikin sa, da abin da muka yaxa a cikinsa na alheri ga talikai.**

**72 Mun yi masa baiwa da Annabi Ishaq a yayin da ya roqi Ubangijinsa ya azurta shi da xa, kuma muka yi masa baiwa da Annabi Yaqub qari a kan haka. Kuma kowanne cikinsu daga Annabi Ibrahim da 'ya'yansa guda biyun: Annabi Ishaq da Annabi Yaqub duka mun mayar da su nagartattu masu biyayya ga Allah.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Halaccin amfani da dabara domin bayyana gaskiya da vata qarya. 2 - Mavarnata suna liqe wa wasu abubuwa da suke riyawa a matsayin hujja a gare su, alhali hujja ce a kansu. 3 - Zafafa harshe cikin zance, wata hanya ce cikin hanyoyin gyara varna, matukar ba zai jawo wata varna wadda ta fi shi girma ba. 4 - Komawa zuwa ga amfani da qarfi, dalili ne akan gazawa wajen fito-na-fito da hujja. 5 - Nasarar Allah ga bayinsa muminai, da tsamar da su daga masifu ta inda ba sa zato.**

وَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَئِمَّةٗ يَهۡدُونَ بِأَمۡرِنَا وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡهِمۡ فِعۡلَ
ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَإِقَامَ ٱلصَّلَوٰةِ وَإِيتَآءَ ٱلزَّكَوٰةِۖ وَكَانُواْ لَنَا
عَٰبِدِينَ ٧٣ وَلُوطًا ءَاتَيۡنَٰهُ حُكۡمٗا وَعِلۡمٗا وَنَجَّيۡنَٰهُ مِنَ
ٱلۡقَرۡيَةِ ٱلَّتِي كَانَت تَّعۡمَلُ ٱلۡخَبَٰٓئِثَۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمَ سَوۡءٖ
فَٰسِقِينَ ٧٤ وَأَدۡخَلۡنَٰهُ فِي رَحۡمَتِنَآۖ إِنَّهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
٧٥ وَنُوحًا إِذۡ نَادَىٰ مِن قَبۡلُ فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ فَنَجَّيۡنَٰهُ
وَأَهۡلَهُۥ مِنَ ٱلۡكَرۡبِ ٱلۡعَظِيمِ ٧٦ وَنَصَرۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡقَوۡمِ
ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمَ سَوۡءٖ فَأَغۡرَقۡنَٰهُمۡ
أَجۡمَعِينَ ٧٧ وَدَاوُۥدَ وَسُلَيۡمَٰنَ إِذۡ يَحۡكُمَانِ فِي ٱلۡحَرۡثِ
إِذۡ نَفَشَتۡ فِيهِ غَنَمُ ٱلۡقَوۡمِ وَكُنَّا لِحُكۡمِهِمۡ شَٰهِدِينَ ٧٨
فَفَهَّمۡنَٰهَا سُلَيۡمَٰنَۚ وَكُلًّا ءَاتَيۡنَا حُكۡمٗا وَعِلۡمٗاۚ وَسَخَّرۡنَا
مَعَ دَاوُۥدَ ٱلۡجِبَالَ يُسَبِّحۡنَ وَٱلطَّيۡرَۚ وَكُنَّا فَٰعِلِينَ ٧٩
وَعَلَّمۡنَٰهُ صَنۡعَةَ لَبُوسٖ لَّكُمۡ لِتُحۡصِنَكُم مِّنۢ بَأۡسِكُمۡۖ
فَهَلۡ أَنتُمۡ شَٰكِرُونَ ٨٠ وَلِسُلَيۡمَٰنَ ٱلرِّيحَ عَاصِفَةٗ تَجۡرِي بِأَمۡرِهِۦٓ
إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ٱلَّتِي بَٰرَكۡنَا فِيهَاۚ وَكُنَّا بِكُلِّ شَيۡءٍ عَٰلِمِينَ ٨١



**(73) Muka mayar da su jagorori waxanda mutane suke shiriya ta hanyarsu zuwa alheri. Suna kiran mutane zuwa ga bautar Allah shi kaxai, da izinin Allah maxaukakin Sarki. Kuma mun yi musu wahayin cewa su yi alheri, kuma ku tsayar da sallah ta fuskar da ta fi kamala, ku bayar da zakka. Kuma sun kasance masu biyayya a gare mu.**

**(74) Haka ma Annabi Lux (A.S) mun ba shi iya raba shari'ah tsakanin masu husuma, kuma mun ba shi ilimin sha'anin addininsa, kuma mun quvutar da shi daga azabar da muka saukar a kan mutanen garinsa (Sadum) wanda mutanen garin suka kasance suna aikata alfasha, lallai sun kasance mutane ne mavarnata, masu fice wa daga xa'ar Ubangijinsu.**

**(75) Kuma mun shigar da shi cikin rahamar mu yayin da muka tserar da shi daga azabar da ya shafe mutanensa. Lallai ya kasance xaya cikin nagartattu masu bin umarnin mu, da hanuwa da haninmu.**

**(76) Kuma ka ambaci qissar Annabi Nuhu (A.S) – Ya kai wannan Manzo-, yayin da ya kira Ubangijinsa tun gabanin Annabi Ibrahim da Annabi Luxu (A.S), sai muka amsa masa, ta hanyar biya masa buqatarsa, muka kuvutar da mutanensa muminai daga vaqin ciki mai girma.**

**(77) Muka tserar da shi daga makircin mutanen da suke qaryata abin da muka qarfafa shi da shi na ayoyin da suke nuna gaskiyarsa. Lallai sun kasance mutane ne mavarnata, masu sharri, sai muka halakar da su gaba xaya da dulmiyar wa a cikin ruwan Xufana.**

**(78) Kuma ka ambaci labarin Annabi Dawud da xan sa Annabi Sulaiman (A.S) – Ya kai wannan Manzo- yayin da suke yin hukunci cikin mas'alar da aka kai qara wurinsu, na wasu masu husuma guda biyu, xayansu yana da tumaki, da suka shiga gonar wani da daddare, suka yi masa varna. Mun kasance masu shaida ne akan hukuncin da suka yi. Babu wani abu na su da yake vuya a gare mu.**

**(79) Sai muka fahimtar da Annabi Sulaiman mas'alar ban da babansa Annabi Dawud. Amma dukkanin su mun ba su Annabta da ilimin hukuncin Shari'ah, ba mun keve Sulaiman ne, shi kaxai ba, kuma mun sanya duwatsu suna tasbihi da tasbihin Annabi Dawud, kuma mun sanya tsuntsaye suna masa biyayya. Kuma mu ne masu bayar da fahimta, da bayar da hikima da ilimi da horewa.**

**(80) Mun sanar da Annabi Dawud ban da Annabi Sulaiman sana'ar yin sulke, don ya kare ku daga fatattakawar makami ga jikinku. Shin – Ya ku mutane- ba zaku zama masu godiya ga Allah ba, akan ni'mar da ya yi muku ba?!.**

**(81) Mun hore wa Annabi Sulaiman Iska mai tsananin bugawa, wadda take gudana da umarninsa zuwa qasar Sham, wadda muka saka albarka a cikinta, ta Annabawan da muka tayar da su a cikinta, da abin da aka shimfixa a cikinta na alherai. Kuma mun kasance Masana ne dangane da komai, babu wani abin da yake vuya gare mu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin aikin alheri da sallah da zakka suna daga cikin abubuwan da Shari'un da suka sauka daga sama suka yi tarayya a ciki.**

**2 - Aikata alfasha sababi ne na aukuwar azabar qare dangi.**

**3 - Nagarta sababi ce na shiga cikin rahamar Allah.**

**4 - Addu'a sababi ce na tsira dag vaqin ciki.**

وَمِنَ ٱلشَّيَٰطِينِ مَن يَغُوصُونَ لَهُۥ وَيَعْمَلُونَ عَمَلًا دُونَ
ذَٰلِكَ ۖ وَكُنَّا لَهُمْ حَٰفِظِينَ ٨٢ ۞ وَأَيُّوبَ إِذْ نَادَىٰ
رَبَّهُۥٓ أَنِّى مَسَّنِىَ ٱلضُّرُّ وَأَنتَ أَرْحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ٨٣
فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ فَكَشَفْنَا مَا بِهِۦ مِن ضُرٍّ ۖ وَءَاتَيْنَٰهُ أَهْلَهُۥ
وَمِثْلَهُم مَّعَهُمْ رَحْمَةً مِّنْ عِندِنَا وَذِكْرَىٰ لِلْعَٰبِدِينَ
٨٤ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِدْرِيسَ وَذَا ٱلْكِفْلِ ۖ كُلٌّ مِّنَ ٱلصَّٰبِرِينَ
٨٥ وَأَدْخَلْنَٰهُمْ فِى رَحْمَتِنَآ ۖ إِنَّهُم مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٨٦
وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبًا فَظَنَّ أَن لَّن نَّقْدِرَ عَلَيْهِ
فَنَادَىٰ فِى ٱلظُّلُمَٰتِ أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبْحَٰنَكَ إِنِّى
كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٧ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ وَنَجَّيْنَٰهُ
مِنَ ٱلْغَمِّ ۚ وَكَذَٰلِكَ نُـۨجِى ٱلْمُؤْمِنِينَ ٨٨ وَزَكَرِيَّآ
إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥ رَبِّ لَا تَذَرْنِى فَرْدًا وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْوَٰرِثِينَ
٨٩ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ وَوَهَبْنَا لَهُۥ يَحْيَىٰ وَأَصْلَحْنَا
لَهُۥ زَوْجَهُۥٓ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ يُسَٰرِعُونَ فِى ٱلْخَيْرَٰتِ
وَيَدْعُونَنَا رَغَبًا وَرَهَبًا ۖ وَكَانُوا۟ لَنَا خَٰشِعِينَ ٩٠

ثلاثة أرباع الحزب ٣٣



**(82) Mun hore wasu daga cikin Shaixanu waxanda suke yi masa nitso a cikin tekuna, suna fito masa da lu'u-lu'u da wasunsu, kuma suna masa wasu ayyukan daban, kamar gini. Kuma mun kasance dangane da adadinsu da ayyukansu masu kiyaye wa ne.**

**(83) Ka ambaci qissar Annabi Ayyuba (A.S) – Ya kai wannan Manzo- yayin da ya kira Ubangijinsa mai tsarki, lokacin da jarabawar cuta ta shafe shi, ya na cewa: “Ya Ubangijina, Lallai an jarrabe ni da cuta, da rashin iyali, kuma kai ne mafi jin qan masu jin qai, ka kawar mini abin da abin da ya auku min na wannan jarrabawa”.**

**(84) Sai muka amsa addu'arsa, muka kawar masa da abin da ya same shi na ciwo, muka ba shi abin da ya rasa na iyalansa da 'ya'yansa, Muka ba shi wasu kwatankwancinsu tare da su, duk wannan mun yi masa ne, saboda wata rahama daga wurinmu, kuma domin wa'azi ga duk wani mai biyayya ga Allah da bauta, domin ya yi haquri kamar yadda Annabi Ayyuba ya yi haquri.**

**(85) Kuma ka ambaci Annabi Isma'il da Annabi Idris da Annabi Zul Kiflu (A.S) – Ya kai wannan Manzo -, kowanne daga cikinsu xaya ne daga cikin masu haquri akan bala'i, da tsayuwa akan duk abin da Allah ya xora musu, su aikata.**

**(86) Mun shigar da su cikin rahamar mu. Muka sanya su Annabawa, kuma muka shigar da su Aljanna. Lallai suna cikin bayin Allah nagartattu, waxanda suke aikin biyayya ga Ubangijinsu, kuma zukatansu da zahirin ayyukansu sun gyaru.**

**(87) Ka ambaci qissar Ma'abocin kifi, Annabi Yunusa (A.S) – Ya kai wannan Manzo -, yayin da ya tafi ba tare da izinin Ubangijinsa ba, yana mai fushi da mutanensa, saboda zarcewarsu cikin savo, sai ya yi zaton cewa ba zamu quntata masa, da yi masa uquba a kan tafiyarsa ba, sai aka jarrabe shi da tsananin qunci, ta tsarewa yayin da kifi ya haxiye shi, sai ya yi addu'a a cikin duhun cikin kifi da teku da dare, yana mai tabbatar da zunubinsa, yana tuba zuwa ga Allah, ya ce: “Babu abin bauta da gaskiya sai kai, tsarki ya tabbata a gare ka, lallai na kasance cikin cikin azzalumai”.**

**(88) Sai muka amsa addu'arsa, muka kuvutar da shi daga baqin ciki, ta hanya fitar da shi daga duhu akan duhu da ya shiga, daga cikin kifi. Irin wannan kuvutarwar da muka yi wa Annabi Yunusa daga baqin cikinsa, haka muke kuvutar da muminai, idan sun faxa cikin baqin ciki kuma suka yi addu'a.**

**(89) Ka ambaci qissar Annabi Zakariyya (A.S) – Ya kai wannan Manzo-, yayin da ya kira Ubangijinsa tsarki ya tabbata a gare shi, yana cewa: “Ya Ubangijina, Kar ka bar ni, ni kaxai, ba ni da xa, lallai kai ne mafi alherin masu wanzuwa, ka azurta ni da xa, wanda zai rayu a bayana”.**

**(90) Sai muka amsa masa addu'arsa, muka ba shi Annabi yahaya a matsayin xa, muka gyara masa matarsa, ta zama mai haihuwa bayan da bakararra ce, ba ta haihuwa. Lallai Annabi Zakariyya da matarsa da xansa sun kasance masu rigegeniya ne wajen aikata alheri, kuma sun kasance suna kiranmu, suna masu fatan abin da ke wurinmu na lada, suna masu tsoron a abin da ke wurinmu na uquba. Kuma sun kasance masu qanqan da kai ne a gare mu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Nagarta sababi ne na rahama**

**2 - Komawa zuwa ga Allah hanya ce ta yaye baqin ciki.**

**3 - Falalar neman xa, domin ya rayu bayan mutuwar mutum.**

**4 - Yin iqrari da zunubi, da jin tsananin buqatuwa zuwa ga Allah, da kokawa dangane da yanayi zuwa gare shi, da biyayya ga Allah cikin walwala, suna daga cikin sababin amsa addu'a, da kawar da bala'i da baqin ciki.**

وَٱلَّتِيٓ أَحۡصَنَتۡ فَرۡجَهَا فَنَفَخۡنَا فِيهَا مِن رُّوحِنَا
وَجَعَلۡنَٰهَا وَٱبۡنَهَآ ءَايَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٩١ إِنَّ هَٰذِهِۦٓ
أُمَّتُكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَأَنَا۠ رَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُونِ ٩٢
وَتَقَطَّعُوٓاْ أَمۡرَهُم بَيۡنَهُمۡۖ كُلٌّ إِلَيۡنَا رَٰجِعُونَ ٩٣
فَمَن يَعۡمَلۡ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَا كُفۡرَانَ
لِسَعۡيِهِۦ وَإِنَّا لَهُۥ كَٰتِبُونَ ٩٤ وَحَرَٰمٌ عَلَىٰ قَرۡيَةٍ
أَهۡلَكۡنَٰهَآ أَنَّهُمۡ لَا يَرۡجِعُونَ ٩٥ حَتَّىٰٓ إِذَا فُتِحَتۡ
يَأۡجُوجُ وَمَأۡجُوجُ وَهُم مِّن كُلِّ حَدَبٖ يَنسِلُونَ ٩٦
وَٱقۡتَرَبَ ٱلۡوَعۡدُ ٱلۡحَقُّ فَإِذَا هِيَ شَٰخِصَةٌ أَبۡصَٰرُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ يَٰوَيۡلَنَا قَدۡ كُنَّا فِي غَفۡلَةٖ مِّنۡ هَٰذَا بَلۡ كُنَّا
ظَٰلِمِينَ ٩٧ إِنَّكُمۡ وَمَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
حَصَبُ جَهَنَّمَ أَنتُمۡ لَهَا وَٰرِدُونَ ٩٨ لَوۡ كَانَ
هَٰٓؤُلَآءِ ءَالِهَةٗ مَّا وَرَدُوهَاۖ وَكُلّٞ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٩٩
لَهُمۡ فِيهَا زَفِيرٞ وَهُمۡ فِيهَا لَا يَسۡمَعُونَ ١٠٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ
سَبَقَتۡ لَهُم مِّنَّا ٱلۡحُسۡنَىٰٓ أُوْلَٰٓئِكَ عَنۡهَا مُبۡعَدُونَ ١٠١



**91 Ka ambaci qissar Nana Maryam (A.S) – Ya kai wannan Manzo-, wadda da katange farjinta daga zina, sai Allah Maxaukakn Sarki ya aika mata da Mala'ika Jibrilu (A.S), sai ya yi mata busa, sai ta yi cikin Annabi Isa (A.S), kuma ta kasance, ita da xanta Annabi Isa alamu ne ga mutane akan ikon Allah, da kuma cewa babu wani abin da zai gagare shi, ta yadda ya halicce shi ba tare da uba ba.**

**92 Lallai wannan shi ne addininku – Ya ku mutane - addini ne guda xaya, shi ne tauhidi, kuma shi ne addinin Musulunci. Kuma Ni ne Ubangijinku. Don haka kun tsarkake bauta a gare ni, ni kaxai.**

**93 Sai mutane suka rarrabu, aka samu mai tauhidi a cikinsu da mushiriki da kafiri. Duka waxannan masu rabuwa xin, zuwa gare mu ne kaxai za a mayar da su a ranar alqiyama, sai mu saka musu akan ayyukansu.**

**94 Duk wanda ya yi aiki nagari a cikinsu, kuma ya yi imani da Allah da Manzanninsa, da ranar lahira, to babu musu dangane da aikinsa na qwarai, Allah zai gode masa akan aikinsa, ya ruvanya masa ladansa, wanda zai same shi a cikin littafin aikinsa a ranar da za a tayar da shi, sai ya yi farin ciki da shi.**

**95 kuma abin da ba zai yiwu ba ne ga duk wata alqarya da muka halaka ta, saboda kafircin mutanenta, su dawo duniya, domin su tuba, a karvi ayyukansu.**

**96 Ba za su dawo ba har abada, har ma idan an buxe bangon Yajuju da Majuju, waxanda a lokacin za su dinga fitowa daga kowane tudu na bayan qasa da sauri.**

**97 Kuma alqiyama ta kusa sakamakon fitowarsu, kuma abubawan ban tsoro da tsananinta za su bayyana, kawai sai ka ga idanun kafirai sun bubbuxe saboda tsananin tsoronta, suna cewa: "Kaiconmu mun halaka, lallai mun kasance a gidan duniya muna cikin wargi da shagala, ba mu shirya wa wannan rana mai girma ba. Bari dai, mun kasance azzalumai saboda kafirci da aikata savo.**

**98 Lallai ku - Ya ku mushirikai da abin da kuke bauta wa koma bayan Allah, na gumaka, da waxanda suka yarda da bautar da kuke yi musu cikin mutane da aljannu- makamashin wutar Jahannama ne, ku da abubuwan bautarku zaku shiga cikinta.**

**99 Da, waxannan abubuwan bautar, sun cancanci bauta ta gaskiya, da ba su shiga wuta ba, su da waxanda suke bauta musu. Amma dukkaninsu da abun bautar, da masu bautar, duk suna wuta, za su zauna a cikinta har abada, ba za su fita ba.**

**100 Zasu rinqa yin wani numfashi mai tsanani –saboda tsananin abin da za su ci karo da shi na zafi-, kuma suna cikin wutar ba sa jin muryar, saboda tsananin tsoro da firgita.**

**101 Yayin da Mushirikai suka ce: (Ai Annabi Isa da Mala'iku ma an bauta musu, don haka su ma za su shiga wuta kenan?) Sai Allah ya ce: "Lallai waxanda ya gabata a cikin ilimin Allah cewa su 'yan aljanna ne, irin su Annabi Isa (A.S) su za a nesantar da su daga wuta".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Fito da matsayin kamewa da bayanin falalar hakan.**

**2 - Haxuwar saqonnin da suka zo daga sama akan kaxaita Allah da ginshiqan bauta.**

**3 - Buxe ganuwar yajuju da Majuju yana daga cikin manya - manyan alamomin tashin alqiyama.**

**4 - Rafkana daga shiri don ranar lahira sababi ne na shan wahalar azabarta.**

لَا يَسْمَعُونَ حَسِيسَهَا ۖ وَهُمْ فِي مَا اشْتَهَتْ أَنفُسُهُمْ
خَالِدُونَ ﴿١٠٢﴾ لَا يَحْزُنُهُمُ الْفَزَعُ الْأَكْبَرُ وَتَتَلَقَّاهُمُ
الْمَلَائِكَةُ هَٰذَا يَوْمُكُمُ الَّذِي كُنتُمْ تُوعَدُونَ ﴿١٠٣﴾
يَوْمَ نَطْوِي السَّمَاءَ كَطَيِّ السِّجِلِّ لِلْكُتُبِ ۚ كَمَا بَدَأْنَا
أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُ ۚ وَعْدًا عَلَيْنَا ۚ إِنَّا كُنَّا فَاعِلِينَ ﴿١٠٤﴾ وَلَقَدْ
كَتَبْنَا فِي الزَّبُورِ مِن بَعْدِ الذِّكْرِ أَنَّ الْأَرْضَ يَرِثُهَا
عِبَادِيَ الصَّالِحُونَ ﴿١٠٥﴾ إِنَّ فِي هَٰذَا لَبَلَاغًا لِّقَوْمٍ
عَابِدِينَ ﴿١٠٦﴾ وَمَا أَرْسَلْنَاكَ إِلَّا رَحْمَةً لِّلْعَالَمِينَ
﴿١٠٧﴾ قُلْ إِنَّمَا يُوحَىٰ إِلَيَّ أَنَّمَا إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَاحِدٌ ۖ فَهَلْ
أَنتُم مُّسْلِمُونَ ﴿١٠٨﴾ فَإِن تَوَلَّوْا فَقُلْ آذَنتُكُمْ عَلَىٰ سَوَاءٍ ۖ
وَإِنْ أَدْرِي أَقَرِيبٌ أَم بَعِيدٌ مَّا تُوعَدُونَ ﴿١٠٩﴾ إِنَّهُ يَعْلَمُ
الْجَهْرَ مِنَ الْقَوْلِ وَيَعْلَمُ مَا تَكْتُمُونَ ﴿١١٠﴾ وَإِنْ أَدْرِي
لَعَلَّهُ فِتْنَةٌ لَّكُمْ وَمَتَاعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿١١١﴾ قَالَ رَبِّ احْكُم
بِالْحَقِّ ۗ وَرَبُّنَا الرَّحْمَٰنُ الْمُسْتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ﴿١١٢﴾

آياتها ٧٨ سُورَةُ الحَجِّ ترتيبها ٢٢



(102) Qarar wutar Jahannama bata isa kunnuwansu. Kuma su masu zama ne cikin abin da rayukansu suke so, na ni'imomi da jin daxi, ni'marsu ba zata yanke ba har abada.

(103) Babban firgici a gare su yayin da wuta zata rufe da 'ya'yanta. Mala'iku za su fuskance su, suna taya su murna, cewa: “Wannan shi ne ranar ku, wadda kuka kasance ana muku alqawarinta a duniya, ana muku albishirin abin da zaku samu a cikinta na ni'ima”.

(104) Ranar da za mu naxe sama kamar yadda ake naxe takarda da abin da ke cikinta, kuma mu tara talikai a irin yanayin da aka haliccesu a cikinta a karon farko. Alqawarinmu babu savawa a cikinsa. Lallai Mun kasance masu cika abin da muka yi alqawari da shi.

(105) Kuma tabbas mun rubuta a cikin littattafan da muka saukar da su ga Manzanni, bayan mun rubuta shi a cikin lahul Mahfuz cewa: “Haqiqa qasa, bayin Allah nagari, masu aiki da xa'arsa, su ne zasu gaje ta, kuma su ne al'ummar Annabi Muhammad (S.A.W).

(106) Lallai cikin abin da muka saukar da shi akwai isarwa zuwa ga mutane masu bautar Ubangijinsu da abin da ya shar'anta musu, domin su ne masu amfana da shi.

(107) Kuma ba mu aiko ka ba – Ya kai Muhammad- face sai don ka zama rahama ga talikai, saboda abubuwan da ka siffantu da su na kwaxayin shiriyar da mutane, da kuvutar da su daga azabar Allah.

(108) Ka ce – Ya kai wannan Manzo-: “Abin da ake mini wahayi da shi, shi ne kawai cewa: “Wanda ya cancanta ku bauta masa da gaskiya, abin bauta ne guda xaya kacal, ba shi da abokin tarayya, kuma shi ne Allah, don haka ku miqa wuya, ku yi imani da shi, da aiki da biyayya a gare shi”.

(109) Idan waxannan suka juya baya daga abin da ka zo musu da shi, to ka ce musu – Ya kai wannan Manzo -: “Ina sanar da ku cewa ni da ku, muna akan wani lamari na rabuwa, wanda muke daidai a cikinsa. Kuma ban san yaushe ne abin da Allah ya yi narkonsa na azaba zai sauka a kanku ba”.

(110) Lallai Allah ya san abin da kuka bayyana na zance, kuma ya san abin da kuka voye cikinsa, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai yi muku sakayya a kansa.

(111) Kuma ban sani ba tana iya yiwu wa jinkirta muku azaba jarabawa ce a gare ku, da talala, da kuma xan jin daxi a gare ku, zuwa wani lokaci qayyadadde a ilimin Allah, domin ku qara zurfi cikin kafircinku da vatanku.

(112) Manzon Allah (S.A.W) ya ce, yana roqon Ubangijinsa: “Ya Ubangijina, ka raba hukunci tsakanina da mutane na, waxanda suka doge akan kafirci, da hukunci na gaskiya. Kuma a wurin Ubangijinmu mai rahama muke neman agaji dangane da abin da kafirai suke faxa na kafirci da qaryatawa”.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Nagarta sababi ne na tabbatuwa a bayan Qasa.
2 - Aiko da Annabi (S.A.W) da Shari'arsa da Sunnarsa jin qai ne ga talikai.
3 - Manzon Allah (S.A.W) bai san gaibu ba.
4 - Sanin Allah da duk abin da yake fitowa daga bayinsa na zance.

# Suratul Hajji

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Ambaton girman Allah Maxaukakin Sarki, da miqa wuya ga Allah, ta hanyar bijiro da abubuwa masu girma da nuna ikon Allah**

## Tafsir:

**1 Ya ku mutane, ku ji tsoron Ubangijinku, ta hanyar kamanta abin da ya umarce ku, da barin abin da ya hana ku. Haqiqa abin da zai zo tare da alqiyama na girgizar qasa da waninta na firgita abu ne mai girma, wajibi ne a yi masa tanadi da aikata abin da Allah ya yarda da shi.**

**2 Ranar da zaku gan ta, dukkan wata shayarwa ta shagala daga barin jaririnta, kuma kowace mai ciki zata yi varin cikinta saboda tsananin tsoro. Kuma zaka ga mutane saboda gushewar hankalinsu kamar bugaggu, saboda tsananin tsoron tsayuwan alqiyama, ba saboda shan giya ba, sai dai azabar Allah mai tsananni ce, ta tafiyar da hankulansu.**

**Yayin da Allah ya ambaci abin da yake tare da tashin alqiyama na abubuwan tsoro da firgita, sai ya mayar da martani ga waxanda suke inkarin tashin alqiyama da tayar da rayuka bayan mutuwa, ya ce:**

**3 Akwai wasu masu jayayya dangane da ikon Allah akan rayar da mutane bayan mutuwa, ba tare da wani sani da suke dogara a kansa ba, kuma suna bin duk wani Shaixan mai taurin kai da jagororin vata cikin aqidar su da zancen su.**

**4 An rubutawa wannan mai taurin kai daga cikin Shaixanun mutane da aljannu cewa duk wanda ya bi shi, ya gasgata shi, to zai vatar da shi daga tafarkin shiriya, ya kuma ja shi zuwa azabar wuta, saboda abin da yake masa jagora da shi na kafirci da savo.**

**5 Ya ku mutane, in har kuna da wata shakka a kan ikonmu na taryar da ku bayan mutuwa, to ku yi tunani cikin halittarku mana, mun halicci babanku Annabi Adam daga turvaya, sannan muka halicci zuri'yarsa daga maniyyin da namiji yake zubawa a mahaifar mace, sannan sai xigon maniyyin ya juya ya zama daskararren jini, sannan xigon jinin ya juya ya zama tsokar nama, kamar tsokar naman da aka tattauna shi, sannan tsokar naman ta juya ta zama cikakkiyar halitta, wadda zata wanzu a cikin mahaifa, har ta fito a matsayin xa mai rai, ko kuma ta zama wata halitta ba cikakkiya ba, wadda mahaifa za ta yi varinta, don mu bayyana muku ikon mu na halittarku a mataki bayan mataki, kuma muna tabbatar da abin da muka ga dama na xan tayi a cikin mahaifa, zuwa wani lokaci qayyadadde, shi ne wata tara, har a haife shi, sannan sai mu fitar da ku daga cikin uwayenku a matsayin jirirai, har ku kai cikar qarfi da hankali, kuma akwai waxanda za su mutu a cikinku kafin nan, akwai kuma waxanda za su rayu har su kai shekarun tsufa tukuf, lokacin da hankali da qarfi za su yi rauni, har su koma zuwa ga wani yanayi da yafi na jariri muni, ba za su san wani abin da da sun san shi ba. Kuma za ka ga qasa a bushe, babu tsiro a cikin ta, amma idan mun saukar da ruwan sama a kanta sai ta girgiza ta fito da tsirrai, qasar ta yi sama, saboda girman 'ya'yan tsirrai, ta fitar da kowane irin dangin tsiro mai kyau da daxin kallo.**

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الحزب ٣٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمۡۚ إِنَّ زَلۡزَلَةَ ٱلسَّاعَةِ شَيۡءٌ عَظِيمٞ
١ يَوۡمَ تَرَوۡنَهَا تَذۡهَلُ كُلُّ مُرۡضِعَةٍ عَمَّآ أَرۡضَعَتۡ وَتَضَعُ
كُلُّ ذَاتِ حَمۡلٍ حَمۡلَهَا وَتَرَى ٱلنَّاسَ سُكَٰرَىٰ وَمَا هُم
بِسُكَٰرَىٰ وَلَٰكِنَّ عَذَابَ ٱللَّهِ شَدِيدٞ ٢ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن
يُجَٰدِلُ فِي ٱللَّهِ بِغَيۡرِ عِلۡمٖ وَيَتَّبِعُ كُلَّ شَيۡطَٰنٖ مَّرِيدٖ ٣
كُتِبَ عَلَيۡهِ أَنَّهُۥ مَن تَوَلَّاهُ فَأَنَّهُۥ يُضِلُّهُۥ وَيَهۡدِيهِ
إِلَىٰ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمۡ فِي رَيۡبٖ
مِّنَ ٱلۡبَعۡثِ فَإِنَّا خَلَقۡنَٰكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ
ثُمَّ مِنۡ عَلَقَةٖ ثُمَّ مِن مُّضۡغَةٖ مُّخَلَّقَةٖ وَغَيۡرِ مُخَلَّقَةٖ لِّنُبَيِّنَ
لَكُمۡۚ وَنُقِرُّ فِي ٱلۡأَرۡحَامِ مَا نَشَآءُ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى ثُمَّ
نُخۡرِجُكُمۡ طِفۡلٗا ثُمَّ لِتَبۡلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمۡۖ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ
وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ أَرۡذَلِ ٱلۡعُمُرِ لِكَيۡلَا يَعۡلَمَ مِنۢ
بَعۡدِ عِلۡمٖ شَيۡـٔٗاۚ وَتَرَى ٱلۡأَرۡضَ هَامِدَةٗ فَإِذَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡهَا
ٱلۡمَآءَ ٱهۡتَزَّتۡ وَرَبَتۡ وَأَنۢبَتَتۡ مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ٥



## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin yin tanadi da guzurin tsoron Allah don ranar alqiyama (taqawa). 2 - Tsananin ban tsoron ranar alqiyama ta yadda mai shayarwa zata manta da jaririnta, mai ciki ta yi barinsa, hankulan mutane su gushe.**

**3 - Sanu-sannu wajen yin halitta sunna ce ta Allah.**

**4 - Kafa hujja da halittar farko akan yiwuwar tayar da rai bayan mutuwa.**

**5 - Ruwan sama da abin da yake biyo bayansa, na fitar da tsirrai dalili ne bayyananne na yiwuwar tashin matattu.**

ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّهُۥ يُحْيِ ٱلْمَوْتَىٰ وَأَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ
قَدِيرٌ ٦ وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ لَّا رَيْبَ فِيهَا وَأَنَّ ٱللَّهَ يَبْعَثُ مَن فِى
ٱلْقُبُورِ ٧ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى
وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ٨ ثَانِىَ عِطْفِهِۦ لِيُضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ لَهُۥ فِى
ٱلدُّنْيَا خِزْىٌ ۖ وَنُذِيقُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ عَذَابَ ٱلْحَرِيقِ ٩ ذَٰلِكَ
بِمَا قَدَّمَتْ يَدَاكَ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيْسَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ١٠ وَمِنَ ٱلنَّاسِ
مَن يَعْبُدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ حَرْفٍ ۖ فَإِنْ أَصَابَهُۥ خَيْرٌ ٱطْمَأَنَّ بِهِۦ ۖ وَإِنْ
أَصَابَتْهُ فِتْنَةٌ ٱنقَلَبَ عَلَىٰ وَجْهِهِۦ خَسِرَ ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةَ ۚ ذَٰلِكَ
هُوَ ٱلْخُسْرَانُ ٱلْمُبِينُ ١١ يَدْعُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَضُرُّهُۥ
وَمَا لَا يَنفَعُهُۥ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلضَّلَٰلُ ٱلْبَعِيدُ ١٢ يَدْعُوا۟ لَمَن
ضَرُّهُۥٓ أَقْرَبُ مِن نَّفْعِهِۦ ۚ لَبِئْسَ ٱلْمَوْلَىٰ وَلَبِئْسَ ٱلْعَشِيرُ ١٣
إِنَّ ٱللَّهَ يُدْخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٍ
تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ١٤ مَن كَانَ
يَظُنُّ أَن لَّن يَنصُرَهُ ٱللَّهُ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ فَلْيَمْدُدْ بِسَبَبٍ إِلَى
ٱلسَّمَآءِ ثُمَّ لْيَقْطَعْ فَلْيَنظُرْ هَلْ يُذْهِبَنَّ كَيْدُهُۥ مَا يَغِيظُ ١٥



**(6) Wannan abin da muka ambata muku- na fakon halitta da matakanta da yanayin waxanda ake haifa daga cikin ku- Mun faxa muku ne saboda ku yi imani da cewa Allah wanda ya halicce ku shi ne gaskiyar da babu shakka a tattare da shi, savanin abin da kuke bautawa na gumakan ku. Kuma domin ku yi imani da cewa Allah yana raya matattu, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagarar shi.**

**(7) Kuma don ku yi imani da cewa tashin alqiyama yana nan tafe, zai zo, babu shakka cikin zuwansa, kuma cewa Allah yana tayar da mamata daga qaburburansu, don ya saka musu akan ayyukansu.**

**Yayin da Allah tsarki ya tabbata a gare shi ya ambaci halin vatattu, waxanda suka vata a dalilin makauniyar biyayya a aya ta uku (3), sai kuma ya ambaci halin jagorarin kafirci a wannan ayar, ya ce:**

**(8) A cikin kafirai akwai waxanda suke jayyaya cikin kaxaita Allah, ba tare da wani ilimi ba, wanda za su iya isa da shi zuwa ga gaskiya, kuma ba tare da bin wani mai shiriya wanda zai nuna musu gaskiya ba, kuma ba tare da wani littafi mai haske wanda aka saukar daga wurin Allah, da zai shiryar da su zuwa ga gaskiya ba.**

**(9) Yana mai juya wuyansa saboda girman kai, domin ya kawar da mutane daga imani da shiga addinin Allah. Duk wanda wannan ita ce siffarsa to yana da wani qasqanci a duniya, na abin da zai gamu da shi na azaba, kuma zamu xanxana masa azabar wuta mai quna a lahira.**

**(10) Kuma a ce masa: "Wannan azabar da ka xanxana, saboda abin da ka aikata ne na kafirci da savo. Allah baya azabta wani daga cikin halittarsa, sai da wani zunubi". (11) A cikin mutane akwai wanda yake ruxaxxe ne, yana bauta wa Allah ne akan shakka, idan alheri ya same shi na lafiya da wadata, sai ya zarce akan imaninsa da bauta wa Allah, in kuma jarrabawa ta same shi, ta ciwo da talauci sai ya camfa addininsa, ya yi ridda. Ya yi hasarar duniyarsa, don kafircinsa ba zai qara masa wani rabo a duniya ba, wanda ba a rubuta masa ba, kuma ya yi hasarar lahirarsa, saboda abin da zai gamu da shi na azabar Allah. Wannan ita ce hasara bayyananniya. (12) Yana bautar wasu gumaka ne koma bayan Allah, waxanda ba za su iya cutar da shi ba, in ya sava musu, ba za su iya amfanar da shi ba in ya yi musu biyayya. Wannan irin bauta da kira ga gumaka shi ne vata mai nisa daga gaskiya.**

**(13) Wannan kafirin da yake bautar gumaka yana kiran wanda cutarwarsa ta fi kusa da amfaninsa, wanda babu shi. Lallai wannan abin bauta wanda cutarwar sa ta fi kusa da amfanarwarsa ya munana, haka nan wanda yake neman taimakonsa shi ma ya munana, haka nan wanda ya zama tare da shi shi ma ya munana.**

**(14) Haqiqa Allah zai shigar da waxanda suka yi imani da shi, kuma suka aikata ayyuka masu kyau Aljannatai, waxanda qoramu ke gudana a qarqashin gine-ginensu. Lallai Allah Maxaukakin Sarki yana aikata abin da ya ga dama na jin qai ga wanda ya yi masa jin qai, da uquba ga wanda ya yi masa uquba, babu wanda zai tilasta shi.**

**(15) Duk wanda yake zaton cewa Allah ba zai bai wa Annabinsa (S.A.W) nasara a duniya da lahira ba, to ya miqa igiyarsa zuwa saman rufin gidansa, sannan ya shaqe kansa da ita, ta hanyar raba kansa da qasa, sannan ya duba ya gani, shi hakan zai tafiyar masa da abin da yake ji a zuciyarsa na fushi. Lallai dai Allah mai bayar da nasara ne ga Annabinsa, ko abokin hamayya ya so ko ya qi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Sabubban shiriya su ne: Ilimi wanda za a kai ga gaskiya da shi, ko mai shiryarwa wanda zai nuna musu hanya, ko wani littafi wanda aka sakankance da shi, wanda zai shiryar zuwa ga gaskiya. 2 - Girman kai hali ne wanda yake hana dace zuwa ga gaskiya. 3 - Yana daga cikin adalcin Allah kasancewarsa baya uquba sai bisa laifi da zunubi. 4 - Allah zai taimaki Manzonsa da addininsa ko da kafirai ba sa son hakan.**

وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَٰهُ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖ وَأَنَّ ٱللَّهَ يَهۡدِي مَن يُرِيدُ
١٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلصَّٰبِـِٔينَ وَٱلنَّصَٰرَىٰ
وَٱلۡمَجُوسَ وَٱلَّذِينَ أَشۡرَكُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ يَفۡصِلُ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ
ٱلۡقِيَٰمَةِۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ١٧ أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ
يَسۡجُدُۤ لَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱلشَّمۡسُ
وَٱلۡقَمَرُ وَٱلنُّجُومُ وَٱلۡجِبَالُ وَٱلشَّجَرُ وَٱلدَّوَآبُّ وَكَثِيرٞ مِّنَ
ٱلنَّاسِۖ وَكَثِيرٌ حَقَّ عَلَيۡهِ ٱلۡعَذَابُۗ وَمَن يُهِنِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن
مُّكۡرِمٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَفۡعَلُ مَا يَشَآءُ ۩ ١٨ ۞ هَٰذَانِ خَصۡمَانِ سجدة ربع الحزب ٣٤
ٱخۡتَصَمُواْ فِي رَبِّهِمۡۖ فَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ قُطِّعَتۡ لَهُمۡ ثِيَابٞ
مِّن نَّارٖ يُصَبُّ مِن فَوۡقِ رُءُوسِهِمُ ٱلۡحَمِيمُ ١٩ يُصۡهَرُ بِهِۦ
مَا فِي بُطُونِهِمۡ وَٱلۡجُلُودُ ٢٠ وَلَهُم مَّقَٰمِعُ مِنۡ حَدِيدٖ ٢١ كُلَّمَآ
أَرَادُوٓاْ أَن يَخۡرُجُواْ مِنۡهَا مِنۡ غَمٍّ أُعِيدُواْ فِيهَا وَذُوقُواْ عَذَابَ
ٱلۡحَرِيقِ ٢٢ إِنَّ ٱللَّهَ يُدۡخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ يُحَلَّوۡنَ فِيهَا مِنۡ
أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٖ وَلُؤۡلُؤٗاۖ وَلِبَاسُهُمۡ فِيهَا حَرِيرٞ ٢٣



**(16) Kamar yadda muka bayyana muku hujjoji bayyanannu akan yiwuwar tashi bayan mutuwa, haka muka saukar wa Annabi Muhammad (S.A.W) Alqur'ani, ayoyi bayyanannu, kuma Allah yana shiryar da wanda ya ga dama da falalarsa zuwa ga tafarkin shiriya.**

**(17) Lallai waxanda suka yi imani da Allah cikin wannan al'umma da yahudawa da Sabiyawa (wasu vangare ne na mabiya wasu Annabawa) da Nasara da masu bautar wuta, da masu bautar gumaka – Haqiqa Allah zai yi hukunci a tsakaninsu a rannar alqiyama, sai ya shigar da muminai Aljannah, ya shigar da wasunsu wuta. Haqiqa Allah mai shaida ne akan dukkan maganganun bayinsa da ayyukansu, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai yi musu sakayya a kai.**

**(18) Baka sani ba – Ya kai wannan Manzo – cewa: “Waxanda suke sama daga Mala’iku suna yi wa Allah sujjada ta biyayya, haka nan waxanda suke qasa daga mutane da aljannu, Rana ma tana masa sujjada, Wata ma yana masa sujjada, Taurarin da suke sama suna masa sujjada, da Duwatsu da Bishiyoyi da Dabbobin a bayan qasa, duka suna masa sujjada ta miqa wuya, , haka ma da yawa daga cikin mutane suna masa sujjada ta xa'a da biyayya, kuma da yawa suna qin yi masa sujjadar biyayya, sai azabar Allah ta tabbata a kansu saboda kafircinsu. Duk wanda Allah ya qaddara masa qasqanci da wulaqanci saboda kafircinsa, to ba shi da wanda zai girmama shi. Lallai Allah yana aikata abin da ya ga dama, babu mai tursasa shi.**

**Yayin da Allah ya bayyana waxanda suke yi masa sujjada bisa xa'a, da waxanda suke qin yi masa, sai ya faxi sakamakon kowa daga cikinsu, ya ce:**

**(19) Waxannan vangarori guda biyu, masu jayayya akan Ubangijinsu, wanene mai gaskiya a cikinsu, vangaren masu imani da vangaren kafirci. Vangaren kafirci wuta ce za ta kewaye su, kamar yadda riga take kewaye da jikin wanda yake sanye da ita, kuma ana kwarara musu ruwan da ya kai qarshe wajen tafasa, a saman kawunansu.**

**(20) Ana narkar da abin da ke cikinsu na hanji soboda tsananin zafinsa, kuma yana isa zuwa fatunsu ya narkar da su.**

**(21) Kuma suna da gudumomi na qarfe a cikin wuta, Mala'iku suna dukansu da su a kan kawunansu.**

**(22) Duk yayin da suka yi qoqarin fita daga wuta saboda tsananin abin da suke gamuwa da shi na baqin ciki, sai a mayar da su cikinta, kuma aka ce musu: “Ku xanxani azabar wuta mai tsananin quna”.**

**(23) Vangaren imani kuma sune waxanda suka yi imani da Allah, suka aikata ayyuka nagari, Allah zai shigar da su cikin wasu Aljannatai, waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu da bishiyoyinsu, Allah zai qawata su da ado na awarwaron zinari da lu'lu', kuma tufafinsu zasu kasance na alhariri ne a cikinsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Shiriya a hannun Allah take, yana kyautar da ita ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa.**

**2 - Saka idon Allah akan komai na ayyukan bayinsa da yanayinsu.**

**3 - Miqa wuyan talikai gaba xayansa ga Allah akan yadda ya tsara, da miqa wuyan muminai a gare shi do yi masa xa'a da biyayya.**

**4 - Azaba tana saukowa ne akan ma'abota kafirci da savo. Rahama kuwa ta tabbata akan ma'abota imani da xa'a.**

وَهُدُوٓاْ إِلَى ٱلطَّيِّبِ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ وَهُدُوٓاْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡحَمِيدِ
٢٤ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسۡجِدِ
ٱلۡحَرَامِ ٱلَّذِي جَعَلۡنَٰهُ لِلنَّاسِ سَوَآءً ٱلۡعَٰكِفُ فِيهِ وَٱلۡبَادِۚ
وَمَن يُرِدۡ فِيهِ بِإِلۡحَادِۭ بِظُلۡمٖ نُّذِقۡهُ مِنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ
٢٥ وَإِذۡ بَوَّأۡنَا لِإِبۡرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلۡبَيۡتِ أَن لَّا تُشۡرِكۡ
بِي شَيۡـٔٗا وَطَهِّرۡ بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ
ٱلسُّجُودِ ٢٦ وَأَذِّن فِي ٱلنَّاسِ بِٱلۡحَجِّ يَأۡتُوكَ رِجَالٗا وَعَلَىٰ
كُلِّ ضَامِرٖ يَأۡتِينَ مِن كُلِّ فَجٍّ عَمِيقٖ ٢٧ لِّيَشۡهَدُواْ
مَنَٰفِعَ لَهُمۡ وَيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡلُومَٰتٍ
عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۖ فَكُلُواْ مِنۡهَا
وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡبَآئِسَ ٱلۡفَقِيرَ ٢٨ ثُمَّ لۡيَقۡضُواْ تَفَثَهُمۡ
وَلۡيُوفُواْ نُذُورَهُمۡ وَلۡيَطَّوَّفُواْ بِٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ ٢٩
ذَٰلِكَۖ وَمَن يُعَظِّمۡ حُرُمَٰتِ ٱللَّهِ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّهُۥ عِندَ
رَبِّهِۦۗ وَأُحِلَّتۡ لَكُمُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ إِلَّا مَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡۖ
فَٱجۡتَنِبُواْ ٱلرِّجۡسَ مِنَ ٱلۡأَوۡثَٰنِ وَٱجۡتَنِبُواْ قَوۡلَ ٱلزُّورِ ٣٠



**(24) Allah ya shiryar da su a rayuwar duniya zuwa ga kyakkyawan zance, kmar shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, da kabbara, da hamdala, kuma ya shiryar da su zuwa ga tafarkin musulunci abin yabo.**

**(25) Haqiqa waxanda suka kafirce wa Allah, kuma suna hana kawar da wasu daga shiga musulunci, kuma suna hana mutane zuwa masallaci mai alfarma, kamar yadda mushirikai suka aikata a shekarar da aka yi sulhun Hudaibiyya, to da sannu zamu xanxana musu azaba mai raxaxi, wannan masallaci mai alfarma shi ne muka sanya shi alqibla ga mutane yayin sallolinsu, da kuma ibada daga ibadodin su na hajji da umara, xan Makka mazaunin gari daidai yake da baqon da ya zo wanda ba xan makka ba, kuma duk wanda ya yi nufin karkacewa gaskiya a cikinsa ta hanyar aikata wani abu na savo da gangan, to zamu xanxana masa azaba mai raxaxi.**

**(26) Ya kai wannan Manzo- ka ambaci yayin da muka bayyana wa Annabi Ibrahim (S.A.W) wurin xaki mai alfarma da iyakokinsa, bayan ba a san shi ba, muka yi masa wahayin cewa kar ka yi shirka da wani abu wajen bauta ta. Ka bauta mini ni kaxai, kuma ka tsarkake xakina daga najasa ta zahiri da ta voye, saboda masu xawafi da masu salla a cikinsa.**

**(27) Kuma ka yi yekuwa ga mutane, kana kiransu zuwa ga ziyarar wanna xaki, wanda muka umarce ka da gina shi, za su zo akan sawunsu, ko a haye kan kowane irin raqumi, ramamme saboda gajiyar tafiya. Raquma za su zo suna xauke da su daga kowace irin hanya mai nisa.**

**(28) Don su shaida abin da zai amfane su na gafarar zunubbai, da samun lada, da haxin kai, da sauransu, kuma domin su ambaci sunan Allah akan abubuwan da za su yanka na Hadaya a kwanaki sanannu, wanda su ne: goma ga watan Zul-Hijja da kwanaki uku bayansa, saboda godiya ga Allah akan abin da ya azurta su da shi na Raquma da Shanu da Awaki. To ku ci daga waxannan dabbobin hadayar, kuma ku ciyar da duk wanda ya kasance mai tsananin talauci daga gare su.**

**(29) Sannan su cika da abin da ya rage musu na aikin hajji, daga nan sai su kwance ihraminsu ta hanyar aske gashin kawunansu, da yanke farcensu, da gusar da dattin da ya taru a cikinsa sakamakon ihrami, kuma domin su sauke nauyin da suka xora wa kawunansu na Hajji da Umara da Hadaya, kuma su yi xawaful Ifada a xakin da Allah ya 'yanta shi daga mamayewar azzaluman shugabanni.**

**(30) Wannan abin da aka umarce ku da shi – na kwance ihrami, da aske gashi, da yanke farce, da gusar da datti, da cika bakance, da xawafi a xakin Allah - shi ne abin da Allah ya wajabta muku. Don haka ku girmama abin da Allah ya wajabta muku. Duk wanda ya nesanci abin da Allah ya umarce shi da ya nesanta, a halin ihraminsa, don girmama iyakokin Allah, da tsoron kar ya qetare su, ya nisanci haramun bai faxa cikinsu ba, to wannan shi ne mafi alheri a gare shi duniya da lahira, a wurin Ubangijinsa tsarki ya tabbata a gare shi. Kuma an halatta muku – Ya ku mutane- dobbobin ni'ima na daga Raquma da Shanu da Awaki, ba a haramta muku wata komai daga cikinsu ba, irin su haami ko bahira ko wasila. Babu abin da ya haramta daga cikinsu sai abin da kuka same shi cikin Alqur'ani, na haramta cin mushe da jini da sauransu. Don haka ku nisanci qazanta, wadda ita ce gumaka. Ku nisanci duk wani zance na qarya da varna ga Allah ko ga bayinsa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Alfarmar xaki mai alfarma wadda take wajabta kulawa da kamewa daga savo a cikinsa, sama da wani wurin wanda ba shi ba. 2 - Xakin Allah mai alfarma matattarar zukatan muminai ne a kowane zamani da lokaci. 3 - Amfanin Hajji yana komawa ga mutane ne, sawa'un amfanin duniya ko na Lahira. 4 - Godewa ni'ima yana wajabta tausayin gajiyayyu.**

حُنَفَاءَ لِلَّهِ غَيْرَ مُشْرِكِينَ بِهِۦ ۚ وَمَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ فَتَخْطَفُهُ ٱلطَّيْرُ أَوْ تَهْوِى بِهِ ٱلرِّيحُ فِى مَكَانٍ سَحِيقٍ
٣١ ذَٰلِكَ ۖ وَمَن يُعَظِّمْ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ فَإِنَّهَا مِن تَقْوَى ٱلْقُلُوبِ ٣٢
لَكُمْ فِيهَا مَنَٰفِعُ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ثُمَّ مَحِلُّهَآ إِلَى ٱلْبَيْتِ ٱلْعَتِيقِ
٣٣ وَلِكُلِّ أُمَّةٍ جَعَلْنَا مَنسَكًا لِّيَذْكُرُوا۟ ٱسْمَ ٱللَّهِ عَلَىٰ
مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلْأَنْعَٰمِ ۗ فَإِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ فَلَهُۥٓ
أَسْلِمُوا۟ ۗ وَبَشِّرِ ٱلْمُخْبِتِينَ ٣٤ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتْ
قُلُوبُهُمْ وَٱلصَّٰبِرِينَ عَلَىٰ مَآ أَصَابَهُمْ وَٱلْمُقِيمِى ٱلصَّلَوٰةِ
وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ٣٥ وَٱلْبُدْنَ جَعَلْنَٰهَا لَكُم مِّن شَعَٰٓئِرِ
ٱللَّهِ لَكُمْ فِيهَا خَيْرٌ ۖ فَٱذْكُرُوا۟ ٱسْمَ ٱللَّهِ عَلَيْهَا صَوَآفَّ ۖ فَإِذَا وَجَبَتْ
جُنُوبُهَا فَكُلُوا۟ مِنْهَا وَأَطْعِمُوا۟ ٱلْقَانِعَ وَٱلْمُعْتَرَّ ۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرْنَٰهَا
لَكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ٣٦ لَن يَنَالَ ٱللَّهَ لُحُومُهَا وَلَا دِمَآؤُهَا
وَلَٰكِن يَنَالُهُ ٱلتَّقْوَىٰ مِنكُمْ ۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرَهَا لَكُمْ لِتُكَبِّرُوا۟
ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمْ ۗ وَبَشِّرِ ٱلْمُحْسِنِينَ ٣٧ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ يُدَٰفِعُ نصف الحزب ٣٤
عَنِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ خَوَّانٍ كَفُورٍ ٣٨



**(31)** **Ku nisanci hakan, kuna masu karkata daga kowane irin addini, wanda yake savanin addininsa, wanda yake yardajje a wurinsa, ba tare da kun haxa wani da shi a cikin bauta ba. Duk wanda ya haxa Allah da wani, to tamkar ya faxo ne daga sama, ko dai tsuntsaye su yayyaga namansa da qasusuwansa, ko kuma iska ta jefa shi cikin wani wuri mai nisan gaske.**

**(32)** **Wancan shine abin da Allah ya yi umarni da shi, na kaxaita shi da bauta, da tsarkake zuciya gare shi, da nesantar gumaka da qarya. Kuma wanda ya girmama alamomin addini – daga cikinsu akwai hadaya da aikin hajji – to ya sani girmama su yana daga cikin abin da yake nuna zukata suna tsoron Ubangijinsu.**

**(33)** **Kuna da amfani da yawa cikin dabbobin hadaya da kuke soke su, a wajen xaki mai alfarma, irin su hawa kansu da fatunsu, da 'ya'yansu, da nononsu, zuwa wani lokaci da aka iyakance shi da lokacin yanka su kusa da xaki mai alfarma, wanda Allah ya 'yanta shi daga mamayewar azzalumai masu girman kai.**

**(34)** **Mun sanya kowace al'umma da ta gabata wurin yanka, da suke zubar da jini a wurin, don neman kusanci zuwa ga Allah, da fatan za su ambaci sunan Allah a kan abubuwan da suke yankawa na neman kusanci a lokacin yankan, saboda nuna godiya ga Allah akan abin da ya azurta su da shi na Raquma da Shanu da Awaki. Don haka abin bautarku da gaskiya – Ya ku mutane- abin bauta ne guda xaya, ba shi da abokin tarayya. Shi kaxai ne kawai za ku sallama masa da miqa wuya, da biyayya a gare shi. Kuma – Ya kai wannan Manzo- ka yi wa masu jin tsoron Allah da tsarkake niyya abishirin abin da zai faranta musu rai.**

**(35)** **Waxanda idan aka ambaci Allah sai su tsoraci uqubarsa, su nesanci sava ma umarninsa, su tsayar da salla cikakkiya, kuma suna haquri idan bala'i ya shafe su, kuma suna ciyarwa a hanyoyin kirki, daga cikin abin da Allah ya azurta su da shi.**

**(36)** **Raquma da Shanun da ake bayar da su hadaya a wajen xaki mai alfarma, mun sanya muku su cikin alamomin addini. Kuna da amfani na addini da na duniya a cikinsu. Don haka ku ce: "Bismillahi yayin soke su, bayan kun jera qafafunsu cikin sahu, suna tsaye, an xaure xaya xaya daga cikin qafafun dabbar, saboda kar ta gudu. Idan sun faxi a gefe xaya, bayan an soke su, to ku ci daga gare su - Ya ku masu hadaya -, kuma ku bai wa talaka wanda yake kamewa baya tambaya, da talakan da yake bin mutane domin a ba shi daga ciki. Kamar yadda Muka hore muku su, don ku xora musu kaya, ku hau kansu, haka muka hore muku su, suke muku biyayya zuwa inda za ku soke su, don neman kusanci ga Allah, ko kwa godewa Allah akan ni'mar hore muku su da ya yi.**

**(37)** **Naman abin da kuke gabatarwa na hadaya da jininsa ba za su isa wurin Allah ba, ba za a xaga su zuwa wurinsa ba, tsoron Allah da kuke da shi ake xagawa zuwa gare shi, don haka ku tsarkake niyyoyinku cikin neman kusanci da su zuwa ga Allah. Haka Allah ya hore muku su, domin ku girmama Allah, ku gode masa bisa abin da ya yi muku na dace zuwa ga gaskiya. Kuma – Ya kai wannan Manzo- ka yi albishir ga masu kyautatawa cikin bautar Ubangijinsu da zamantakewarsu da bayinsa, albishirin da abin da zai faranta musu rai.**

**(38)** **Allah yana kare waxanda suka yi imani da shi daga sharrin aboka gabarsu. Lallai Allah ba ya son duk wani mai yawan ha'intar amanarsa, mai yawan butulci ga ni'mominsa, marar godiya ga Allah, yana fushi da shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Buga misali don kusanto da abubuwan da ba a gani, ta hanyar mayar da su kamar waxanda ake gani, babbar hanya ce ta tarbiyya. 2 - Falalar qanqan da kai (Tawali'u). 3 - Kyautatawa a cikin ayyukan ibada sababi ne na samun rabo. 4 - Imani sababi ne da Allah yake kare bawansa saboda shi, kuma ya kula da shi.**

أُذِنَ لِلَّذِينَ يُقَٰتَلُونَ بِأَنَّهُمۡ ظُلِمُواْۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ نَصۡرِهِمۡ لَقَدِيرٌ
٣٩ ٱلَّذِينَ أُخۡرِجُواْ مِن دِيَٰرِهِم بِغَيۡرِ حَقٍّ إِلَّآ أَن يَقُولُواْ
رَبُّنَا ٱللَّهُۗ وَلَوۡلَا دَفۡعُ ٱللَّهِ ٱلنَّاسَ بَعۡضَهُم بِبَعۡضٖ لَّهُدِّمَتۡ
صَوَٰمِعُ وَبِيَعٞ وَصَلَوَٰتٞ وَمَسَٰجِدُ يُذۡكَرُ فِيهَا ٱسۡمُ ٱللَّهِ
كَثِيرٗاۗ وَلَيَنصُرَنَّ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ
عَزِيزٌ ٤٠ ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ
وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُواْ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَنَهَوۡاْ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۗ
وَلِلَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلۡأُمُورِ ٤١ وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدۡ كَذَّبَتۡ
قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ وَعَادٞ وَثَمُودُ ٤٢ وَقَوۡمُ إِبۡرَٰهِيمَ وَقَوۡمُ
لُوطٖ ٤٣ وَأَصۡحَٰبُ مَدۡيَنَۖ وَكُذِّبَ مُوسَىٰۖ فَأَمۡلَيۡتُ لِلۡكَٰفِرِينَ
ثُمَّ أَخَذۡتُهُمۡۖ فَكَيۡفَ كَانَ نَكِيرِ ٤٤ فَكَأَيِّن مِّن قَرۡيَةٍ
أَهۡلَكۡنَٰهَا وَهِيَ ظَالِمَةٞ فَهِيَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا وَبِئۡرٖ
مُّعَطَّلَةٖ وَقَصۡرٖ مَّشِيدٍ ٤٥ أَفَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَتَكُونَ
لَهُمۡ قُلُوبٞ يَعۡقِلُونَ بِهَآ أَوۡ ءَاذَانٞ يَسۡمَعُونَ بِهَاۖ فَإِنَّهَا
لَا تَعۡمَى ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَلَٰكِن تَعۡمَى ٱلۡقُلُوبُ ٱلَّتِي فِي ٱلصُّدُورِ ٤٦



**Yayin da Allah ya bayyana cewa yana kare muminai, zukatan su suka samu nutsuwa, sai ya yi musu izini su yaqi kafirai, ya ce:**

**(39) Allah ya yi wa muminai izinin yaqar mushirikan da suke yaqar su, saboda saboda zaluncin da abokan gabarsu suke musu. Lallai Allah mai ikon ba su nasara ne akan abokan gabarsu, ba tare da yaqi ba, amma hikimarsa ta hukunta cewa ya jarraba muminai ta hanyar yaqi da Kafirai.**

**(40) Wanxanda Kafirai suka fitar da su daga gidajensu da zalunci, ba don wani laifi da suka aikata ba, sai dai kawai don sun ce: Ubangijinmu shi ne Allah, ba mu da wani abin bauta koma bayansa. Ba don abin da Allah ya shar'anta wa Annabawansa da muminai na yaqar abokan gabarsu ba, da sun yi ta'addanci a kan wuraren bauta, sun rushe masu bauta wuraren da suke bauta a cikinsu, da da wurare bautar Nasara (Church) da wuraren bautar Yahudawa, da masallatan musulmi, waxanda aka tanada don yin salla, wanda a cikinsu musulmai suke ambaton Allah da yawa. Kuma haqiqa Allah zai taimaki dun wanda ya taimaki addinin sa da Manzonsa. Lallai Allah Mai qarfi ne wajen taimaka wa wanda ya taimaki addininsa, Mabuwayi ne wanda babu wanda zai iya rinjaye a kansa.**

**(41) Wanxannan da aka yi wa alqawarin nasara, su ne waxanda idan mun ba su mulki a bayan qasa, ta hanyar nasara akan abokan gabarsu, sai su tsayar da salla bisa siffa mafi cika, su bayar da zakkar dukiyoyinsu, su yi umarni da abin da Shari'ah ta yi umarni da shi, su hana abin da ta yi hani a kai. Kuma ga Allah shi kaxai makomar lamura take, wajen bayar da lada da yin uquba.**

**(42) Idan mutanenka - Ya kai wannan Manzo - suka qaryata ka, to ka yi haquri, ba kai ne na farko wanda mutanensa suka qaryata shi ba, lallai mutanen Annabi Nuhu a gabaninka sun qaryata Annabi Nuhu, Adawa sun qaryata Annabi Hudu, Samudawa sun qaryata Annabi Salihu.**

**(43) Mutanen Annabi Ibrahim su ma sun qaryata Annabi Ibrahim, Mutanen Annabi Luxu ma sun qaryata Annabi Luxu.**

**(44) Mutanen Madyana su ma sun qaryata Annabi Shu'aibu, Fir'auna da mutanensa sun qaryata Annabi Musa, amma sai na jinkirta wa mutanensu uquba don yi musu talala, sannan na kama su da azaba, to ka yi tunanin yadda na yi musu inkari? Haqiqa na halaka su saboda kafircinsu.**

**(45) Alqaryu nawa ne muka halaka su saboda kafircinsu –suna azzalumai - da azabar qare dangi, ga gidanjensu a rushe, babu mutanensu a cikinsu. Kuma rijiyoyi nawa suka wofinta daga masu xiba ruwa a cikin su, saboda an halaka su. Kuma manyan benaye masu ado guda nawa ne basu iya kare mazaunansu ba daga azaba?!.**

**(46) Shin waxannan masu qaryata abin da Manzon Allah (S.A.W) ya zo da shi, ba su yi tafiya a bayan qasa ba ne , domin su ga guraben waxancan halakakkun alqaryun ba, su yi tunani da hankalinsu, su xauki izina, su ji labaransu ji na wa'azantuwa. Makanta ba ita ce makantar gani ba, a'a, makanta mai halakarwa ita ce makantan basira, ta yadda ma'abocinta ba ya lura ko xaukan wa'azi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tabbatar da siffofin qarfi da izza ga Allah.**
**2 - Tabbatar da shar'anta Jihadi, domin kare wuraren ibada.**
**3 - Tsayar da addini sababi ne na taimakon Allah ga bayinsa muminai.**
**4 - Makantar zuciya tana hana la'akari da ayoyin Allah.**

وَيَسۡتَعۡجِلُونَكَ بِٱلۡعَذَابِ وَلَن يُخۡلِفَ ٱللَّهُ وَعۡدَهُۥۚ وَإِنَّ يَوۡمًا
عِندَ رَبِّكَ كَأَلۡفِ سَنَةٖ مِّمَّا تَعُدُّونَ ٤٧ وَكَأَيِّن مِّن
قَرۡيَةٍ أَمۡلَيۡتُ لَهَا وَهِيَ ظَالِمَةٞ ثُمَّ أَخَذۡتُهَا وَإِلَيَّ ٱلۡمَصِيرُ
٤٨ قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَآ أَنَا۠ لَكُمۡ نَذِيرٞ مُّبِينٞ ٤٩ فَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٥٠
وَٱلَّذِينَ سَعَوۡاْ فِيٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ
ٱلۡجَحِيمِ ٥١ وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٖ وَلَا نَبِيٍّ إِلَّآ
إِذَا تَمَنَّىٰٓ أَلۡقَى ٱلشَّيۡطَٰنُ فِيٓ أُمۡنِيَّتِهِۦ فَيَنسَخُ ٱللَّهُ مَا يُلۡقِي
ٱلشَّيۡطَٰنُ ثُمَّ يُحۡكِمُ ٱللَّهُ ءَايَٰتِهِۦۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٥٢ لِّيَجۡعَلَ
مَا يُلۡقِي ٱلشَّيۡطَٰنُ فِتۡنَةٗ لِّلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ وَٱلۡقَاسِيَةِ
قُلُوبُهُمۡۗ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَفِي شِقَاقِۭ بَعِيدٖ ٥٣ وَلِيَعۡلَمَ
ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَيُؤۡمِنُواْ بِهِۦ
فَتُخۡبِتَ لَهُۥ قُلُوبُهُمۡۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهَادِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِلَىٰ صِرَٰطٖ
مُّسۡتَقِيمٖ ٥٤ وَلَا يَزَالُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي مِرۡيَةٖ مِّنۡهُ حَتَّىٰ
تَأۡتِيَهُمُ ٱلسَّاعَةُ بَغۡتَةً أَوۡ يَأۡتِيَهُمۡ عَذَابُ يَوۡمٍ عَقِيمٍ ٥٥



**(47) Kafirai cikin mutanenka - Ya kai wannan manzo- suna neman ka yi gaggawar kawo musu azaba ta gaggawa a nan duniya, da wadda aka jinkirta a lahira, a duk lokacin da aka yi musu gargaxi da azabar. Tabbas Allah ba zai sava abin da ya yi musu alqawarinsa ba. Abin da ya faru da su a ranar yaqin Badar yana daga cikin na gaggawar. Kuma lallai rana xaya cikin azaba a lahira kamar shekara dubu ce a lissafin shekarun ku na duniya, saboda abin da ke cikinsa na azaba.**
**(48) Alqaryu guda nawa ne na jinkirta musu azaba, alhali sun kasance azzalumai, saboda kafircinsu, ban gaggauta musa azaba ba, na yi yi musu talala, sannan na damqe su da azabar qare dangi, kuma zuwa gare ni ne, ni kaxai makomarsu take a ranar alqiyama, kuma zan saka musu akan kafircinsu da azaba madawwamiya.**
**(49) Ya ku mutane, ni fa mai gargaxi ne a gareku, ina isar muku da abin da aka aiko ni da shi ne, ina bayyana muku gargaxin dalla-dalla.**
**(50) Waxanda suka yi imani da Allah, suka aikata ayyuka nagari, suna da gafarar zunubansu daga wurin Ubangijinsu, kuma suna da wani arziqi na karamci a cikin Aljanna, wanda ba ya yankewa.**
**(51) Waxanda kuma suka yi aiki cikin qaryata ayoyinmu, suna qaddara cewa za su gagare Allah, su quvuce masa, ya kasa azabta su, to waxannan su ne ma'abota wutar Jahim, za ta lazimce shi kamar yadda aboki yake lizimtar abokinsa.**
**(52) Ba mu tava aiko wani Manzo ko Annabi gabaninka ba – Ya kai wannan Manzo- face sai idan yana karanta littafin Allah, sai Shaixan ya jefa wani abu, wanda zai rikitar da mutane da shi a matsayin wani vangare ne na wahayi, amma sai Allah ya vata abin da Shaixan yake jefawa, ya tabbatar da ayoyinsa. Allah Masani ga dukkan komai, babu wani abu wanda yake vuya a gare shi, mai hikima ne cikin halittarsa da qaddarawar sa da gudanarwar sa.**
**(53) Shaixan yana jefa ruxu a cikin karatun Annabin ne, domin abin da ya jefa xin ya zama jarrabawa ga munafikai, da waxanda zukatansu suka qeqashe a cikin mushirikai. Lallai Azzalumai daga munafikai da mushirikai suna cikin gaba da Allah da Manzonsa, kuma sun yi nesa daga gaskiya da shiriya.**
**(54) Kuma don waxanda Allah ya ba su ilimi su samu yaqinin cewa wannan Alqur'anin da aka saukar wa Annabi Muhammad (S.A.W) shi ne gaskiyar da Allah ya yi wahayin ta zuwa gare ka – Ya kai wannan Manzo- sai su qara imani da ita, zukatansu su qara nutsuwa da miqa wuya zuwa gare ta. Lallai Allah mai shiryar da waxanda suka yi imani da shi ne zuwa tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa, a sakamakon miqa wuya da suka yi masa.**
**(55) Waxanda suka karfice wa Allah, suka qaryata Manzonsa ba zasu gushe ba suna cikin shakka dangane da abin da aka saukar maka na Alqur'ani, har alqiyama ta zo musu, ba zato ba tsammani, suna kan hakan, ko kuma azabar ranar da babu rahama da alheri a ciki ta zo musu, ita ce azabar alqiyama.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin talala ga azzalumi har ya su zarce cikin zaluncinsu, sunna ce ta Allah.**
**2 - Kariyar da Allah ya bawa littafinsa daga canji ko musanyawa, da kuma kawar masa da makircin mataimakan shaixan.**
**3 - Munafinci da qeqashewar zuciya, cutuka ne masu kisa.**
**4 - Imani sakamako ne na ilimi, kuma nutsuwa da miqa wuya ga umarnin Allah, shi ne sakamakon imani.**

ٱلۡمُلۡكُ يَوۡمَئِذٖ لِّلَّهِ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٥٦ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٞ
مُّهِينٞ ٥٧ وَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ قُتِلُوٓاْ
أَوۡ مَاتُواْ لَيَرۡزُقَنَّهُمُ ٱللَّهُ رِزۡقًا حَسَنٗاۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ
خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ٥٨ لَيُدۡخِلَنَّهُم مُّدۡخَلٗا يَرۡضَوۡنَهُۥۚ
وَإِنَّ ٱللَّهَ لَعَلِيمٌ حَلِيمٞ ٥٩ ۞ ذَٰلِكَۖ وَمَنۡ عَاقَبَ بِمِثۡلِ
مَا عُوقِبَ بِهِۦ ثُمَّ بُغِيَ عَلَيۡهِ لَيَنصُرَنَّهُ ٱللَّهُۚ إِنَّ ٱللَّهَ
لَعَفُوٌّ غَفُورٞ ٦٠ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي
ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعُۢ
بَصِيرٞ ٦١ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدۡعُونَ
مِن دُونِهِۦ هُوَ ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ٦٢
أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَتُصۡبِحُ ٱلۡأَرۡضُ
مُخۡضَرَّةًۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٞ ٦٣ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ ٱلۡغَنِيُّ ٱلۡحَمِيدُ ٦٤

ثلاثة أرباع الحزب ٣٤



**(56) mulki a ranar alqiyama – ranar da abin da aka yi waxannan alqawarinsa na azaba zai musu-to a ranar mulki na Allah ne shi kaxai, babu mai jayayya da shi a ciki, shi ne shi kaxai zai yi hukunci tsakanin muminai da kafirai, ya yi wa kowa hukunci da abin da ya dace da shi, Waxanda suka yi imani da Allah, suka aikata ayyuka nagartattu, suna da wani lada mai girma, shi ne Aljannatai na ni'ima, na dindindin, waxanda ba sa yankewa.**

**(57) Waxanda kuma suka kafirce wa Allah, suka qaryata ayoyinmu da muka saukar wa Manzannin mu, to suna da wata azaba ta wulaqanci, wadda Allah zai wulaqanta su da ita a wutan Jahannama.**

**(58) Kuma waxanda suka qaurace wa gidajensu da qasashensu, don neman yardar Allah da xaukaka addininsa, sannan aka kashe su a wurin jihadi, don xaukaka kalmar Allah, ko suka mutu, to tabbas Wallahi Allah zai azurta su da wani arziqi kyakkyawa, wanda ba ya yankewa. Kuma lallai Allah tsarki ya tabbata a gare shi shi ne mafi alherin masu azurtawa.**

**(59) Tabbas Allah zai shigar da su wani wuri, wanda za su yarda da shi, shi ne Aljanna. Haqiqa Allah ya san ayyukansu da niyyoyinsu, kuma mai haquri ne, ta yadda bai gaggauta yi musu uquba a kan abubuwan da suka yi sakaci a kansu ba.**

**(60) Wannan abin da aka ambata, na shigar da waxanda suka yi hijira don xaukaka kalmar Allah cikin Aljanna, da yin izinin fuskantar xan ta'adda da irin ta'addancin da ya yi, ta yadda babu laifi akan wanda yayi hakan, to amma idan xan ta'adda ya kuma maimaita ta'addancinsa to lallai Allah zai bayar da nasara ga wanda aka yi wa ta'addanci. Haqiqa Allah mai afuwa ne ga zunuban muminai, mai gafara ne a gare su.**

**(61) Wannan nasara ga wanda aka yi wa ta'addanci, saboda Allah mai iko ne a kan duk abin da ya ga dama, daga cikin ikon sa akwai shigar da dare cikin yini, da yini cikin dare, ta hanya qara xayansu da rage xayan, kuma saboda Allah mai jin zancen bayinsa ne, masanin ayyukansu ne, babu abin da yake vuya a gare shi daga cikinsu, kuma zai saka musu a kai.**

**(62) Wannan abin da aka faxa na shigar da dare cikin yini, da yini cikin dare, yana faruwa ne domin Allah shi ne gaskiya, addininsa gaskiya ne, alqawarinsa gaskiya ne, bayar da nasararsa ga muminai gaskiya ne, kuma abin da mushrikai suke bautawa koma bayan Allah na gumaka shi ne qaryar da bata da tushe, kuma saboda Allah shi ne Maxaukaki akan bayinsa, xaukaka ta zati da girma da iko, mai girma, wanda yake da dukkanin girma da xaukaka.**

**(63) Shin baka gani ba – Ya kai wannan Manzo- Allah ya saukar da ruwan sama daga sama, sai qasa ta zama koriya shar, bayan ruwan sama ya sauka a kanta, ta hanyar abin da take fitar wa na tsirrai. Haqiqa Allah mai tausayin bayinsa, ta yadda yake saukar musu da ruwan sama, ya fitar musu da tsirrai daga qasa. Kuma masani ne dangane da labarinsu, babu wani abu cikinsa da yake vuya gare shi.**

**(64) Shi kaxai yake da mulkin abin da yake sama, da abin da yake qasa. Kuma haqiqa Allah shi ne Mawadaci, wanda ba ya buqatar kowa daga cikin halittarsa, Abin godewa a kowane hali.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Matsayin hijira a Musulunci da falalarta**

**2 - Halaccin rama uquba da irin abin da aka yi maka.**

**3 - Taimakon da Allah yake yi wa wanda aka yi wa ta'addanci yana kasancewa a duniya ko a lahira.**

**4 - Tabbatar da siffofin xaukaka ga Allah, a bisa yadda ya dace da shi, kamar sauran siffofi, irin su ilimi, da ji da ga ni da xaukaka.**

أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱلۡفُلۡكَ تَجۡرِي
فِي ٱلۡبَحۡرِ بِأَمۡرِهِۦ وَيُمۡسِكُ ٱلسَّمَآءَ أَن تَقَعَ عَلَى ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا
بِإِذۡنِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ٦٥ وَهُوَ ٱلَّذِيٓ
أَحۡيَاكُمۡ ثُمَّ يُمِيتُكُمۡ ثُمَّ يُحۡيِيكُمۡۗ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَكَفُورٞ ٦٦
لِّكُلِّ أُمَّةٖ جَعَلۡنَا مَنسَكًا هُمۡ نَاسِكُوهُۖ فَلَا يُنَٰزِعُنَّكَ
فِي ٱلۡأَمۡرِۚ وَٱدۡعُ إِلَىٰ رَبِّكَۖ إِنَّكَ لَعَلَىٰ هُدٗى مُّسۡتَقِيمٖ ٦٧
وَإِن جَٰدَلُوكَ فَقُلِ ٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا تَعۡمَلُونَ ٦٨ ٱللَّهُ يَحۡكُمُ
بَيۡنَكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٦٩
أَلَمۡ تَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۚ إِنَّ
ذَٰلِكَ فِي كِتَٰبٍۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٧٠ وَيَعۡبُدُونَ
مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ بِهِۦ سُلۡطَٰنٗا وَمَا لَيۡسَ لَهُم بِهِۦ
عِلۡمٞۗ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِن نَّصِيرٖ ٧١ وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُنَا
بَيِّنَٰتٖ تَعۡرِفُ فِي وُجُوهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلۡمُنكَرَۖ يَكَادُونَ
يَسۡطُونَ بِٱلَّذِينَ يَتۡلُونَ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِنَاۗ قُلۡ أَفَأُنَبِّئُكُم بِشَرّٖ مِّن
ذَٰلِكُمُۚ ٱلنَّارُ وَعَدَهَا ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ٧٢



**(65) Shin baka gani ba – Ya kai wannan Manzo - Allah ya hore maka kai da mutane duk abin da yake qasa na dabbobi, da daskararrun abubuwa, don amfanin ku da buqatun ku, kuma ya hore muku jiragen ruwa suna gudana a kan teku da umarninsa da horewarsa, suna gudana daga wani gari zuwa wani gari, kuma yana riqe da sama saboda kar ta faxo a kan qasa, sai da izinin sa, da ya yi mata izini ta faxo a kan qasa da ta faxo. Haqiqa Allah mai tausayi ne, mai jin qai ga mutane, ta yanda ya hore musu waxannan abubuwan, duk da abin da suke a kai na zalunci.**

**(66) Allah shi ne wanda ya raya ku, ta yadda ya samar da ku bayan kun kasance babu, sannan kuma zai kashe ku idan shekarun rayuwarku sun cika, sannan zai raya ku bayan mutuwarku domin ya yi muku hisabi a kan ayyukan ku, ya yi muku sakayya a kansu. Lallai mutum mai yawan butulci ne ga ni'imomin Allah – duk da bayyanar su- ta hanyar haxa shi da wani cikin bauta.**

**(67) Mun sanya wa ma'abota kowane addini shari'arsu, don haka suna aiki da shari'arsu, saboda haka kar Mushirikai da mabiya wasu addinai su yi jayayya da kai – Ya kai wannan Manzo- dangane da shari'arka, kai ka fi su cancanta da gaskiya, domin su ma'abota qarya ne, kuma ka kira mutane zuwa kaxaita Allah. Haqiqa kana kan tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa.**

**(68) Kuma idan suka qi sai dai su yi jayayya da kai, bayan hujja ta bayyana a fili, to ka miqa lamarinsu zuwa ga Allah, kana mai cewa - a matsayin jan kunne: "Allah shi ya fi sanin abin da kuke aikatawa na kowane aiki, babu wani abu na ayyukanku da yake vuya a gare shi, kuma zai saka muku a kansu".**

**(69) Allah zai yi hukunci tsakanin bayinsa, muminan su da kafiran su a ranar lahira cikin abin da suka kasance suna savani a kai a rayuwar duniya na lamarin addini.**

**(70) Shin baka sani ba – Ya kai wannan manzo- cewa Allah yana sane da abin da yake sama da abin da yake qasa, babu wani abu a cikin su wanda yake vuya a gare shi. Lallai ilimin hakan yana rubuce a Lauhul mahfuz. Haqiqa ilimin hakan gaba xaya mai sauqi ne a wurin Allah.**

**(71) Mushirikai suna bauta wa gumaka waxanda Allah bai saukar da hujja a kan bautarsu a littafansa ba, kuma ba su da wani dalili na ilimi akan hakan. Madogararsu kawai ita ce kwaikwayon iyayensu ido rufe. Kuma azzalumai ba su da wani mai taimako da zai kare su daga abin da zai auku a kansu na azabar Allah.**

**(72) Idan ana karanta musu bayyanannun ayoyinmu na Alqur'ani, zaka gane inkarinsu a fuskokin waxanda suka kafirta, ta inda za su vata ran su yayin da suke jin waxannan ayoyi, saura qiris su damqi waxanda suke karanta musu ayoyin mu. To ka ce musu - Ya kai wannan Manzo-: "Shin in baku labarin abin da ya fi fushinku da vata ranku sharri? Shi ne: "Wutar da Allah ya yi wa kafirai alqawarin zai shigar da su cikinta. Kuma tir da wannan makoma da za su koma gare ta".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yana daga cikin ni'imomin Allah a kan mutane: hore musu da duk abin da yake sama da qasa.**
**2 - Tabbatar da siffofin tausayi da jin qai ga Allah.**
**3 - kewayewar ilimin Allah da abin da yake sama da qasa da tsakaninsu.**
**4 - Makauniyar biyayya ita ce sababin da ya sa mushirikai suke riqe shirkar su ga Allah.**

يَا أَيُّهَا النَّاسُ ضُرِبَ مَثَلٌ فَاسْتَمِعُوا لَهُ إِنَّ الَّذِينَ
تَدْعُونَ مِن دُونِ اللَّهِ لَن يَخْلُقُوا ذُبَابًا وَلَوِ اجْتَمَعُوا لَهُ
وَإِن يَسْلُبْهُمُ الذُّبَابُ شَيْئًا لَّا يَسْتَنقِذُوهُ مِنْهُ ضَعُفَ
الطَّالِبُ وَالْمَطْلُوبُ ٧٣ مَا قَدَرُوا اللَّهَ حَقَّ قَدْرِهِ إِنَّ اللَّهَ
لَقَوِيٌّ عَزِيزٌ ٧٤ اللَّهُ يَصْطَفِي مِنَ الْمَلَائِكَةِ رُسُلًا
وَمِنَ النَّاسِ إِنَّ اللَّهَ سَمِيعٌ بَصِيرٌ ٧٥ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ
أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَإِلَى اللَّهِ تُرْجَعُ الْأُمُورُ ٧٦ يَا أَيُّهَا
الَّذِينَ آمَنُوا ارْكَعُوا وَاسْجُدُوا وَاعْبُدُوا رَبَّكُمْ
سَجْدَة وَافْعَلُوا الْخَيْرَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ۩ ٧٧ وَجَاهِدُوا فِي
اللَّهِ حَقَّ جِهَادِهِ هُوَ اجْتَبَاكُمْ وَمَا جَعَلَ عَلَيْكُمْ
فِي الدِّينِ مِنْ حَرَجٍ مِّلَّةَ أَبِيكُمْ إِبْرَاهِيمَ هُوَ سَمَّاكُمُ
الْمُسْلِمِينَ مِن قَبْلُ وَفِي هَٰذَا لِيَكُونَ الرَّسُولُ شَهِيدًا عَلَيْكُمْ
وَتَكُونُوا شُهَدَاءَ عَلَى النَّاسِ فَأَقِيمُوا الصَّلَاةَ وَآتُوا الزَّكَاةَ
وَاعْتَصِمُوا بِاللَّهِ هُوَ مَوْلَاكُمْ فَنِعْمَ الْمَوْلَىٰ وَنِعْمَ النَّصِيرُ ٧٨

آياتها ١١٨ — سُورَةُ المُؤْمِنُونَ — ترتيبها ٢٣



**(73) Ya ku mutane! An buga misali, ku saurare shi, ku lura da shi: "Haqiqa waxanda kuke bauta musu, gumaka da sauransu, ba za su tava iya halittar quda ba, duk da qanqantar sa, saboda gazawarsu, ko da gaba xayansu za su taru, don su halicce shi, ba zasu iya halittar sa ba. Kuma in quda za ciri wani abu, daga gare su na turare ko waninsa, ba za su iya qwace shi daga wurin shi ba. Wannan gaza halittar qudan, da rashin iya qwace abubuwansu xin, yana bayyana gazawarsu na yi abin da ya fi wannan girma. To ta yaya zaku bauta musu – duk da gazawarsu- koma bayan Allah?!. Wannan mai nema, wato gunkin da ake masa bauta, wanda ba zai iya qwato abin da quda ya xauke masa ba, mai rauni ne, haka ma wanda ake neman a wurinsa, wato qudan, shi ma mai rauni ne.**

**(74) Ba su girmama Allah matuqar girmamawar da ta dace da shi ba, yayin da suka bauta wa wasu halittarsa tare da shi. Lallai Allah mai qarfi ne, kuma halittar sammai da qassai da abin da ke tsakaninsu yana daga cikin qarfin sa da ikon sa, Mabuwayi ne wanda ba za a iya galaba a kansa ba, savanin gumakan mushirikai, waxanda suke raunana ne, qasqantattu ba sa halittar komai.**

**(75) Allah yana zavar Manzanni daga cikin Mala'iku, haka ma daga cikin Mutane, sai ya tura wasu Malai'iku zuwa wurin Annabawa Mutane, kamar yadda ya tura Mala'ika Jibril zuwa wajen Manzannin mutane, kuma yana tura Manzannin mutane zuwa wajen mutane. Lallai Allah mai jin abin da mushirikai suke faxa ne dangane da Manzanninsa, ya san wanda yake zava don Manzancinsa.**

**(76) Allah yana sane da abin da Manzanninsa cikin Mala'iku da Mutane suke a kai, tun kafin ya halicce su, da bayan mutuwar su, kuma zuwa ga Allah ne kaxai dukkanin lamura za a mayar da su a ranar alqiyama, inda zai tayar da bayinsa, ya saka musu bisa abin da suka gabatar na aiki.**

**(77) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka aikata abin da ya shar'anta musu, ku yi ruku'i, ku yi sujjada a cikin sallar ku don Allah shi kaxai, kuma ku aikata alheri, na sada zumunci da sadaka, da fatan ku rabauta da abin da kuke buqata, ku tsira daga abin da kuke tsoro.**

**(78) Kuma ku yi jihadi saboda Allah, don neman yardar sa, shi ne ya zave ku, ya sanya addininku mai saauqi, babu qunci ko wahala a cikinsa, wannan addini mai sauqin shi ne addinin babanku Annabi Ibrahim (A.S). Allah ne ya kira ku Musulmai a littafan da suka gabata da a cikin Alqur'ani, saboda Manzon Allah ya zama mai shaida a kanku cewa ya isar muku da abin da aka turo shi ya isar muku da shi, kuma domin ku ku zama masu shaida a kan al'ummun da suka gabata, cewa Manzannin su, sun isar musu da saqo. Ku gode wa Allah a kan wannan, ta hanyar tsayar da sallah a bisa siffa cikakkiya, ku bayar da zakkar dukiyoyin ku, ku koma zuwa ga Allah, ku dogara gare shi cikin lamuran ku, domin Allah tsarki ya tabbata a gare shi shi ne mafi kyawun Majivincin lamarin wanda ya jibince shi, cikin muminai, kuma shi ne mafi kyawun mataimaka ga wanda ya nemi taimakonsa, do haka ku jivince shi, zai kula da ku, ku nemi taimakonsa zai taimaka muku.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mahimmanci buga misali don bayyana ma'anoni. Wannan wata hanya ce mai girma ta tarbiyya.**

**2 - Gazawar gumaka wajen halittar mafi qanqantar abu dalili ne na gazawarsu akan halittar waninsa.**

**3 - Rashin girmama Allah shi ne sababin yin shirka gare shi.**

**4 - Tabbatar da siffofin qarfi da izza ga Allah, da mahimmancin mumini ya riqa halarto ma'anonin waxannan siffofi.**